۞ إِلَيۡهِ يُرَدُّ عِلۡمُ ٱلسَّاعَةِۚ وَمَا تَخۡرُجُ مِن ثَمَرَٰتٖ مِّنۡ أَكۡمَامِهَا
وَمَا تَحۡمِلُ مِنۡ أُنثَىٰ وَلَا تَضَعُ إِلَّا بِعِلۡمِهِۦۚ وَيَوۡمَ يُنَادِيهِمۡ أَيۡنَ
شُرَكَآءِي قَالُوٓاْ ءَاذَنَّٰكَ مَا مِنَّا مِن شَهِيدٖ ٤٧ وَضَلَّ عَنۡهُم
مَّا كَانُواْ يَدۡعُونَ مِن قَبۡلُۖ وَظَنُّواْ مَا لَهُم مِّن مَّحِيصٖ ٤٨
لَّا يَسۡـَٔمُ ٱلۡإِنسَٰنُ مِن دُعَآءِ ٱلۡخَيۡرِ وَإِن مَّسَّهُ ٱلشَّرُّ فَيَـُٔوسٞ
قَنُوطٞ ٤٩ وَلَئِنۡ أَذَقۡنَٰهُ رَحۡمَةٗ مِّنَّا مِنۢ بَعۡدِ ضَرَّآءَ مَسَّتۡهُ
لَيَقُولَنَّ هَٰذَا لِي وَمَآ أَظُنُّ ٱلسَّاعَةَ قَآئِمَةٗ وَلَئِن رُّجِعۡتُ إِلَىٰ
رَبِّيٓ إِنَّ لِي عِندَهُۥ لَلۡحُسۡنَىٰۚ فَلَنُنَبِّئَنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ بِمَا عَمِلُواْ
وَلَنُذِيقَنَّهُم مِّنۡ عَذَابٍ غَلِيظٖ ٥٠ وَإِذَآ أَنۡعَمۡنَا عَلَى ٱلۡإِنسَٰنِ
أَعۡرَضَ وَنَـَٔا بِجَانِبِهِۦ وَإِذَا مَسَّهُ ٱلشَّرُّ فَذُو دُعَآءٍ عَرِيضٖ
٥١ قُلۡ أَرَءَيۡتُمۡ إِن كَانَ مِنۡ عِندِ ٱللَّهِ ثُمَّ كَفَرۡتُم بِهِۦ
مَنۡ أَضَلُّ مِمَّنۡ هُوَ فِي شِقَاقِۭ بَعِيدٖ ٥٢ سَنُرِيهِمۡ ءَايَٰتِنَا
فِي ٱلۡأٓفَاقِ وَفِيٓ أَنفُسِهِمۡ حَتَّىٰ يَتَبَيَّنَ لَهُمۡ أَنَّهُ ٱلۡحَقُّۗ
أَوَلَمۡ يَكۡفِ بِرَبِّكَ أَنَّهُۥ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ شَهِيدٌ ٥٣ أَلَآ إِنَّهُمۡ
فِي مِرۡيَةٖ مِّن لِّقَآءِ رَبِّهِمۡۗ أَلَآ إِنَّهُۥ بِكُلِّ شَيۡءٖ مُّحِيطُۢ ٥٤



**(47) Ga Allah shi kaxai ake mayar da ilimin tashin alqiyama, shi ne kaxai yasan yaushe zata faru, ba wanda ya san haka wanda ba shi ba. Babu wani xan itace da zai fita daga vawonsa wanda yake kewaye da shi, haka nan babu wata mace da zata yi ciki ta haihu face ya sani, babu abin da yake kubce masa daga cikin wannan. A ranar da Allah zai kirawo mushrikai, waxanda suke bautawa gumaka tare da shi, yana mai yi musu tsawa a kan bautawa gumakan da suka yi, ya ce: "Ina abokan tarayyata, waxanda kuka kasance kuna riya cewa su ne abokan tarayyata?. Sai mushrikai su ce: "Mun yarda yau a gabanka, babu wani daga cikin mu a yau da yake shaidawa kana da abokin tarayya".**

**(48) Abin da suke bautawa daga gumaka ya vace musu, kuma suka tabbatar cewa basu da matsera daga azabar Allah ko wata mafaka.**

**(49) Mutum baya gajiya da neman lafiya da dukiya da 'ya'ya, da sauran abubuwan da suka yi kama da haka, na daga ni'imomi, idan kuma talauci ko rashin lafiya ko makamancin haka suka same shi, to sai ka gan shi mai yawan xebe qauna daga rahamar Allah ne.**

**(50) Idan kuma muka xanxana masa lafiya daga wajen mu, da wadata da lafiya, bayan bala'i da rashin lafiya da ya same shi, tabbas sai ka ji ya ce: "Wannan dama nawa ne, don ni, na cancanci haka, kuma dama nawa ne, kai! bana tsammanin alqiyama ma zata tashi, kuma ma da ace alqiyamar zata tashi, ai ni a wurin Allah ina da wadata da dukiya, kamar yadda ya yi min ni'ima a duniya, saboda cancantata, to a lahira ma haka zai yi min. Tabbas haqiqa zamu bawa waxanda suke kafirce da Allah labarin abin da suka aikata a duniya, na kafirci da savo, kuma tabbas haqiqa zamu xanxana musu azaba mafi tsanani.**

**(51) Kuma idan muka yi ni'ima ga mutum, ni'imar lafiya, da makamancinta, sai ya rafkana ga barin ambaton Allah da yi masa xa'a, ya bijire yana mai girman kai, amma idan rashin lafiya ko taulaci ko waninsa ya same shi, to fa shi a wannan lokaci mai yawan roqon Allah ne, yana kai kukansa gare shi, a kan abin da ya same shi, don ya yaye masa. Baya godewa Ubangijinsa idan ya yi masa ni'ima, kuma baya yin haquri a kan bala'i idan ya jarrabe shi.**

**(52) Ya kai wannan Manzo, ka cewa waxannan mushirikai masu qaryatawa: "Ku bani labari, idan wannan Alqur'ani daga Allah yake, amma sai kuka kafirce masa, kuka qaryata shi, to yaya halinku zai kasance?". Babu wanda ya fi vata sama da wanda ya yi wa gaskiya taurin kai, bayan ta bayyana qarara, hujjar ta da qarfin ta sun bayyana?!.**

**(53) Da sannu zamu nunawa kafiran quraishawa ayoyin mu, a cikin sasannin qasa, ta hanyar abin da Allah zai yi wa musulmi buxi da shi, kuma mu nuna musu ayoyin mu a karan-kansu, ta hanyar buxe garin Makkah domin ya bayyana a gare su, bayyanar da take xauke shakka cewa wannan Alqur'ani gaskiya ne, wadda babu kokwanto a cikin ta.Yanzu bai ishi waxannan m mushirikai hujja ba cewa wannan Alqur'anin gaskiya ne, saboda shaidar Allah da kansa cewa daga gare shi yake?. Waye ya fi shaida mai girma fiye da Allah?! Da suna nufin gaskiya da sun wadatu da shaidar Ubangijinsu.**

**(54) Ku saurara!. Haqiqa mushirikai suna cikin shakkun haxuwa da Ubangijin su ranar alqiyama, saboda suna qaryata tashi bayan mutuwa, kuma basu yi imani da lahira ba, don haka basa yi mata shiri da aiki na qwarai. Ku saurara! haqiqa Allah ya kewaye komai da ilimi da iko.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Ilimin tashin alqiyama yana wurin Allah shi kaxai. 2 - Yadda kafiri yake mu'amalantar Allah game da ni'ima da bala'i akwai ruxu da harigido a ciki. 3 - Kewayewar Allah ga komai da iko da ilimi.**

آياتها ٥٣ سُورَةُ الشُّورَىٰ ترتيبها ٤٢

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

حمٓ ١ عٓسٓقٓ ٢ كَذَٰلِكَ يُوحِيٓ إِلَيۡكَ وَإِلَى ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِكَ
ٱللَّهُ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ ٣ لَهُۥ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِۖ
وَهُوَ ٱلۡعَلِيُّ ٱلۡعَظِيمُ ٤ تَكَادُ ٱلسَّمَٰوَٰتُ يَتَفَطَّرۡنَ مِن فَوۡقِهِنَّۚ
وَٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ يُسَبِّحُونَ بِحَمۡدِ رَبِّهِمۡ وَيَسۡتَغۡفِرُونَ لِمَن فِي
ٱلۡأَرۡضِۗ أَلَآ إِنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلۡغَفُورُ ٱلرَّحِيمُ ٥ وَٱلَّذِينَ ٱتَّخَذُواْ
مِن دُونِهِۦٓ أَوۡلِيَآءَ ٱللَّهُ حَفِيظٌ عَلَيۡهِمۡ وَمَآ أَنتَ عَلَيۡهِم بِوَكِيلٖ
٦ وَكَذَٰلِكَ أَوۡحَيۡنَآ إِلَيۡكَ قُرۡءَانًا عَرَبِيّٗا لِّتُنذِرَ أُمَّ ٱلۡقُرَىٰ وَمَنۡ
حَوۡلَهَا وَتُنذِرَ يَوۡمَ ٱلۡجَمۡعِ لَا رَيۡبَ فِيهِۚ فَرِيقٞ فِي ٱلۡجَنَّةِ وَفَرِيقٞ فِي
ٱلسَّعِيرِ ٧ وَلَوۡ شَآءَ ٱللَّهُ لَجَعَلَهُمۡ أُمَّةٗ وَٰحِدَةٗ وَلَٰكِن يُدۡخِلُ مَن
يَشَآءُ فِي رَحۡمَتِهِۦۚ وَٱلظَّٰلِمُونَ مَا لَهُم مِّن وَلِيّٖ وَلَا نَصِيرٍ ٨ أَمِ
ٱتَّخَذُواْ مِن دُونِهِۦٓ أَوۡلِيَآءَۖ فَٱللَّهُ هُوَ ٱلۡوَلِيُّ وَهُوَ يُحۡيِ ٱلۡمَوۡتَىٰ وَهُوَ
عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٞ ٩ وَمَا ٱخۡتَلَفۡتُمۡ فِيهِ مِن شَيۡءٖ فَحُكۡمُهُۥٓ
إِلَى ٱللَّهِۚ ذَٰلِكُمُ ٱللَّهُ رَبِّي عَلَيۡهِ تَوَكَّلۡتُ وَإِلَيۡهِ أُنِيبُ ١٠



# Suratush Shura

An Saukar Da Ita A Makkah

## Daga Manufofin Surar:

**Bayanin haqiqanin wahayi da saqon Annabtar Manzon Allah (S.A.W) da bayanin cewa wannan saqo na Manzon Allah ci gaba ne da wahayin da aka yi wa Annabawa gabaninsa.**

## Tafsir:

**(1) (2) (Hamim) ( Ain, Sin, Qaf ) Bayani akan ire-iren waxannan haruffa ya gabata a farkon suratul Baqara.**

**(3) Irin wannan wahayi ne ake yi maka, ya Annabi Muhammad (S.A.W) da kuma waxanda suke gabaninka, daga Annabawan Allah. Allah wanda yake Mabuwayi cikin kamun da yake wa maqiyansa, kuma mai hikima cikin gudanarwar sa da halittarsa.**

**(4) Na Allah ne shi kaxai abin da yake cikin sammai da qassai, halittarsa ne, mulkinsa ne, gudanarwarsa ne, kuma shi ne Maxaukaki da zatinsa, da matsayinsa, da kuma buwayarsa, kuma mai girma a zatinsa.**

**(5) Saboda girmansa (S.W.T) sammai tare da girman su da xaukakar su sun kusa kecewa a saman qassai, Mala'iku kuma suna tsarkake Ubangijinsu suna girmama shi, suna masu gode masa da qasqantar da kai da girmamawa, suna neman gafarar Allah ga mutanen qasa. Ku saurara, haqiqa Allah shi ne mai gafarta wa wanda ya tuba daga cikin bayinsa, kuma mai jin qansu.**

**(6) Waxanda suka riqi gumaka koma bayan Allah, suna jivintar su, suna bauta musu koma bayan Allah, to Allah yana nan yana jiransu, yana rubuta ayyukansu, kuma zai saka musu da su. kuma kai – Ya wannan Manzo – ba wanda aka xorawa kiyaye ayyukan su ba ne, baza a tambaye ka a kan ayyukansu ba, kai xan saqo ne kawai.**

**(7) Kamar yadda muka yi wahayi ga Annabawa a gabaninka – Ya kai wannan Manzo - haka kai ma muka yi maka wahayin Alqur'ani balarabe, don ka gargaxi mutanen Makkah da waxanda suke gefenta daga garuruwan larabawa, sannan mutane gaba xaya, kuma ka tsoratar da mutane game da ranar alqiyama, ranar da Allah zai tara mutanen farko da na qarshe, a fili guda xaya domin yi musu hisabi da sakayya, babu shakka cikin afkuwar hakan, kuma mutane sun kasu gida biyu a wannan ranar: wasu a cikin Aljannah su ne Muminai, wasu kuma a cikin wuta su ne kafirai. (8) Da Allah ya ga damar ya sanya su su zama al'umma xaya, a kan addinin musulunci, da ya sanya su hakan, ya shigar da su Aljannah faba xaya, sai dai hikimarsa ta gudana a kan shigar da wanda ya ga dama a musulunci, kuma ya shigar da shi Aljannah. Waxanda suka zalunci kawunansu da yin kafirci da savon Allah, basu da wanda zai jivinci lamarinsu, basu da wani mataimaki da zai tseratar da su daga azabar Allah.**

**(9) Kawai dai waxannan mushrikai sun riqi wasu koma bayan Allah majivinta lamarinsu, suna son su, amma Allah shi ne abin jivinta na gaskiya, waninsa baya amfanarwa baya cutarwa, kuma shi ne yake raya matattu, don ya yi musu hisabi da sakayya, babu abin da yake gajiyar da shi (S.W.T).**

**(10) Ya ku mutane, duk abin da kuka yi savani a kansa na tushen addinin ku, ko rassansa, to hukuncinsa yana ga Allah, sai a koma ga littafinsa, ko sunnar Manzonsa (S.A.W). Wannan da ya siffantu da wannan siffa shi ne Ubangijina, kuma gare shi na dogara a cikin al'amurana gaba xaya, kuma gare shi nake komawa da tuba.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Girman Allah a bayyane yake a cikin komai. 2 - Addu'ar Mala'iku ta alheri ga masu imani. 3 - Alqu'ani da sunnah ne abin dogaron Muminai a cikin duk al'amuransu, Musamman ma yayin savani. 4 - An kevance gargadi ga mutanen Makkah da kewayenta, saboda su ake yi wa raddi, Saboda inkarinsu ga saqon Manzon Allah (S.A.W), amma shi Manzo ne ga mutane gaba xaya, kamar yadda Allah ya ce: (Ba mu aiko ka ba face sai ga mutane gaba xaya…).**

فَاطِرُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۚ جَعَلَ لَكُم مِّنْ أَنفُسِكُمْ أَزْوَٰجًا
وَمِنَ ٱلْأَنْعَٰمِ أَزْوَٰجًا ۖ يَذْرَؤُكُمْ فِيهِ ۚ لَيْسَ كَمِثْلِهِۦ شَىْءٌ ۖ وَهُوَ
ٱلسَّمِيعُ ٱلْبَصِيرُ ١١ لَهُۥ مَقَالِيدُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۖ يَبْسُطُ
ٱلرِّزْقَ لِمَن يَشَآءُ وَيَقْدِرُ ۚ إِنَّهُۥ بِكُلِّ شَىْءٍ عَلِيمٌ ١٢ ۞ شَرَعَ الحزب ٤٩
لَكُم مِّنَ ٱلدِّينِ مَا وَصَّىٰ بِهِۦ نُوحًا وَٱلَّذِىٓ أَوْحَيْنَآ إِلَيْكَ وَمَا
وَصَّيْنَا بِهِۦٓ إِبْرَٰهِيمَ وَمُوسَىٰ وَعِيسَىٰٓ ۖ أَنْ أَقِيمُوا۟ ٱلدِّينَ
وَلَا تَتَفَرَّقُوا۟ فِيهِ ۚ كَبُرَ عَلَى ٱلْمُشْرِكِينَ مَا تَدْعُوهُمْ إِلَيْهِ ۚ ٱللَّهُ
يَجْتَبِىٓ إِلَيْهِ مَن يَشَآءُ وَيَهْدِىٓ إِلَيْهِ مَن يُنِيبُ ١٣ وَمَا تَفَرَّقُوٓا۟
إِلَّا مِنۢ بَعْدِ مَا جَآءَهُمُ ٱلْعِلْمُ بَغْيًۢا بَيْنَهُمْ ۚ وَلَوْلَا كَلِمَةٌ سَبَقَتْ
مِن رَّبِّكَ إِلَىٰٓ أَجَلٍ مُّسَمًّى لَّقُضِىَ بَيْنَهُمْ ۚ وَإِنَّ ٱلَّذِينَ أُورِثُوا۟
ٱلْكِتَٰبَ مِنۢ بَعْدِهِمْ لَفِى شَكٍّ مِّنْهُ مُرِيبٍ ١٤ فَلِذَٰلِكَ
فَٱدْعُ ۖ وَٱسْتَقِمْ كَمَآ أُمِرْتَ ۖ وَلَا تَتَّبِعْ أَهْوَآءَهُمْ ۖ وَقُلْ
ءَامَنتُ بِمَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ مِن كِتَٰبٍ ۖ وَأُمِرْتُ لِأَعْدِلَ بَيْنَكُمُ ۖ
ٱللَّهُ رَبُّنَا وَرَبُّكُمْ ۖ لَنَآ أَعْمَٰلُنَا وَلَكُمْ أَعْمَٰلُكُمْ ۖ لَا حُجَّةَ
بَيْنَنَا وَبَيْنَكُمُ ۖ ٱللَّهُ يَجْمَعُ بَيْنَنَا ۖ وَإِلَيْهِ ٱلْمَصِيرُ ١٥



**(11) Allah ne mahaliccin sammai da qassai, ba tare da ya kwafa a wurin wani ba, ya sanya ku jinsi biyu, maza da mata, haka nan ya sanya raquma da shanu, da dabbobi, jinsi biyu, maza da mata, domin su yawaita duk saboda ku, yana halittar ku da abin da ya sanya muku na mataye ta hanyar aure, kuma yana raya ku da abin da ya sanya muku na dabbobin ni'ima, daga namansu da nononsu, babu abin da ya yi kama da shi a cikin halittarsa, kuma shi mai ji ne ga maganganun bayinsa, mai ganin ayyukansu, babu abin da yake kuvce masa, kuma zai saka musu a kan ayyukansu, idan alheri ne, su samu alheri, idan sharri ne, su samu sharri.**

**(12) A wurinsa ne kaxai mabuxan taskar sammai da qassai suke, yana yalwata arziki ga wanda ya ga dama daga cikin bayinsa, don ya jarrabe shi, shin zai gode ko kuwa zai butulce?. Kuma yana quntata shi ga wanda ya ga dama, don ya jarraba shi, shin zai yi haquri, ko kuwa zai ji haushin abin da Allah ya qaddara?. Haqiqa shi masani ne a kan komai, babu abin da yake vuya a gare shi na masalahar bayinsa.**

**(13) Ya shar'anta muku daga addini, irin abin da ya umarci Annabi Nuhu da ya isar da shi, da aiki da shi, da abin da muka yi wahayi gare ka - Ya kai wannan Manzo, kuma ya shar'anta muku irin abin da muka umarci Annabi Ibrahim, da Musa, da Isa, su isar da shi, da aiki da shi, wanda a taqaice dai shi ne: ku tsayar da addini, ku bar rarrabuwa a cikinsa, abin da kuke kiran mushirikai zuwa gare shi na kaxaita Allah, da barin bautawa waninsa, ya yi musu girma, Allah yana zavar wanda ya ga dama daga cikin bayinsa, ya datar da shi ga bautarsa, da yi masa xa'a kuma yana shiryar da wanda yake komawa gare shi da tuba daga zunubansa.**

**(14) Kafirai da mushirikai basu rarraba ba, sai bayan da hujja ta tsaya a kansu, da aiko Annabi Muhammad (S.A.W) zuwa gare su, kuma rarrabuwar su bata kasance ba face sai don zalunci da qetare iyaka. Ba don abin da ya rigaya a cikin ilimin Allah na zai jinkirta musu azaba zuwa wani lokaci iyakantacce a wurinsa ba, shi ne ranar alqiyama, da Allah ya yi musu hukunci a tsakaninsu, ya gaggauta musu azaba sakamakon kafircewa Allah, da qaryata Manzanninsa. Haqiqa waxanda aka gadar musu da Attaura daga cikin yahudawa, da Injila daga cikin Nasara, bayan magabatansu, kuma bayan waxannan mushirikai, suna cikin ruxani da shakku game da wannan Alqur'ani, wanda Annabi Muhammad (S.A.W) ya zo da shi, suna qaryata shi.**

**(15) Ka yi kira zuwa ga wannan addini miqaqqe, kuma ka tabbata a kansa gwargwadon yadda Allah ya yi maka umarni, kada ka bi soye-soyen zukatansu na banza, ka ce yayin jayayya da su: "Na yi imani da Allah, da littafan da ya saukar wa Manzanni, kuma Allah ya umarce ni na yi hukunci a tsakaninku da adalci. Allah da nake bautawa shi ne Ubangijina da ku gaba xaya, ayyukanmu namu ne na alheri ne ko sharri, kuma ayyukanku naku ne, na alheri ko sharri, babu sauran wata jayayya a tsakanin mu da ku bayan hujja ta bayyana, hanya ta fito fili, Allah zai tara tsakanin mu da ku gaba xaya, kuma gare shi ne makoma take ranar alqiyama, ya sakawa kowannen mu da abinda ya cancanta da shi, a lokacin sai mai gaskiya ya bayyana daga mai qarya, wanda yake daidai da wanda yake kan varna.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Addinin Annabawa a cikin tushensa duk guda xaya ne.**

**2 - Muhimmancin haxin kai da haxarin rarrabuwa.**

**3 - Daga ginshiqin samun nasarar kira zuwa ga Allah akwai: ingancin manufa, da tsayawa a kanta, da nisantar son zuciya, da yin adalci, da mayar da hankali a kan abin da aka yi tarayya a kansa, da barin jayayya maras amfani, da tunatar da juna makomar da aka yi tarayya a kanta.**

وَٱلَّذِينَ يُحَآجُّونَ فِي ٱللَّهِ مِنۢ بَعۡدِ مَا ٱسۡتُجِيبَ لَهُۥ حُجَّتُهُمۡ
دَاحِضَةٌ عِندَ رَبِّهِمۡ وَعَلَيۡهِمۡ غَضَبٞ وَلَهُمۡ عَذَابٞ شَدِيدٌ
١٦ ٱللَّهُ ٱلَّذِيٓ أَنزَلَ ٱلۡكِتَٰبَ بِٱلۡحَقِّ وَٱلۡمِيزَانَۗ وَمَا يُدۡرِيكَ
لَعَلَّ ٱلسَّاعَةَ قَرِيبٞ ١٧ يَسۡتَعۡجِلُ بِهَا ٱلَّذِينَ لَا يُؤۡمِنُونَ
بِهَاۖ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مُشۡفِقُونَ مِنۡهَا وَيَعۡلَمُونَ أَنَّهَا ٱلۡحَقُّۗ
أَلَآ إِنَّ ٱلَّذِينَ يُمَارُونَ فِي ٱلسَّاعَةِ لَفِي ضَلَٰلِۭ بَعِيدٍ ١٨
ٱللَّهُ لَطِيفُۢ بِعِبَادِهِۦ يَرۡزُقُ مَن يَشَآءُۖ وَهُوَ ٱلۡقَوِيُّ ٱلۡعَزِيزُ
١٩ مَن كَانَ يُرِيدُ حَرۡثَ ٱلۡأٓخِرَةِ نَزِدۡ لَهُۥ فِي حَرۡثِهِۦۖ وَمَن
كَانَ يُرِيدُ حَرۡثَ ٱلدُّنۡيَا نُؤۡتِهِۦ مِنۡهَا وَمَا لَهُۥ فِي ٱلۡأٓخِرَةِ
مِن نَّصِيبٍ ٢٠ أَمۡ لَهُمۡ شُرَكَٰٓؤُاْ شَرَعُواْ لَهُم مِّنَ ٱلدِّينِ
مَا لَمۡ يَأۡذَنۢ بِهِ ٱللَّهُۚ وَلَوۡلَا كَلِمَةُ ٱلۡفَصۡلِ لَقُضِيَ بَيۡنَهُمۡۗ
وَإِنَّ ٱلظَّٰلِمِينَ لَهُمۡ عَذَابٌ أَلِيمٞ ٢١ تَرَى ٱلظَّٰلِمِينَ
مُشۡفِقِينَ مِمَّا كَسَبُواْ وَهُوَ وَاقِعُۢ بِهِمۡۗ وَٱلَّذِينَ
ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ فِي رَوۡضَاتِ ٱلۡجَنَّاتِۖ لَهُم
مَّا يَشَآءُونَ عِندَ رَبِّهِمۡۚ ذَٰلِكَ هُوَ ٱلۡفَضۡلُ ٱلۡكَبِيرُ ٢٢



**(16) Waxanda suke yin jayayya da hujjojin vatattu, a cikin wannan addinin da aka saukarwa Annabi Muhammad (S.A.W) bayan mutane sun amsa masa, waxannan masu yin jayayyar hujjojinsu vatattu ne, kuma a qasa suke warwas a wurin Allah da wurin Muminai, basu da wani tasiri, kuma fushin Allah ya tabbata a kansu saboda kafircinsu da qin gaskiyar su, kuma suna da azaba mai tsanani tana jiran su ranar alqiyama. Yayin da Allah ya bayyana vacin hujjojin kafirai, sai ya bayyana tushen hujjoji masu inganci, waxanda musulmi yake kafa hujja da su, su ne Alqur'ani, ya ce:**

**(17) Allah shi ne wanda ya saukar da Alqur'ani da gaskiyar da babu kokwanto a cikin ta, kuma ya saukar da adalci, don yin hukunci a tsakanin mutane da adalci. Alqiyamar da waxannan suke qaryatawa zata iya kasancewa a kusa, kuma abu ne sananne cewa duk abin da zai zo to a kusa yake.**

**(18) Waxanda basu yi imani da ita ba suna ta neman a gaggauto musu da ita, saboda su basu yi imani da hisabi ko sakayya ko lada ko uquba ba. Waxanda suka yi imani da Allah suna tsoron ta, don tsoron makomar su a cikinta, kuma sun sani, sani na yaqini cewa zuwan ta gaskiya ne, babu shakka a cikin sa. Ku saurara, haqiqa waxanda suke jayayya game da tashin alqiyama, suke husuma a kanta suna cikin vata mai nisa da kaucewa gaskiya.**

**(19) Allah ma'abocin rangwame ne ga bayinsa, yana azurta wanda ya ga dama, sai ya yalwata masa arzikinsa, ya quntatawa wanda ya ga dama, don jin qai a gare shi, koda a bayyane ba haka ba ne. Allah shi ne mai qarfin da babu wanda yake galaba a kansa, Mabuwayi wanda da yake kama maqiyansa,**

**(20) Duk wanda yake son ladan lahira, kuma yayi aiki irin nata, zamu ninka masa ladansa, kyakkyawa xaya a ninka ta goma, har zuwa ninki xari bakwai, zuwa ninki mai yawa. Wanda yake nufin duniya kaxai, zamu bashi iya rabonsa da aka qaddara masa a duniya, kuma ba shi da wani rabo a lahira, domin ya fifita duniya a kan lahira.**

**(21) Ko waxannan mushirikan suna da wasu alloli ne koma bayan Allah, kuma sun shar'anta musu abin da Allah bai yi musu izini a shar'anta shi ba, na yin shirka da shi, da haramta abin da ya halatta, da halatta abin da ya haramta?. Ba don lokacin da Allah ya sanya na yin hukunci a tsakanin masu savani ba, da kuma cewa zai jirkinta musu zuwa gare shi, da ya yi hukunci a tsakaninsu. Haqiqa waxanda suka zalunci kansu da yin shirka da savo suna da azaba mai raxaxi, tana jiran su ranar alqiyama.**

**(22) Ya kai wannan Manzo, zaka ga waxanda suka zalunci kansu da yin shirka da savon Allah suna tsorace da uquba, saboda abin da suka aikata na laifi, kuma uquba sai ta same su babu makawa, tsagwaron tsoro wanda babu tuba a cikinsa ba zai amfane su ba. Waxanda suka yi imani da Allah da Manzanninsa, kuma suka yi ayyuka nagari, suna kan kishiyar abin da waxancan suke kai, suna cikin gonakin Aljannah, cikin ni'ima, suna da duk abin da suke so a wajen Ubangijinsu, na ni'imomi kala-kala, waxanda basa yankewa har abada, wannan shi ne falala babba, wadda babu falalar da ta kai ta.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Tsoron mumini a kan tashin hakalin ranar alqiyama yana taimaka masa wajen yi mata tanadi.**

**2 - Rangwamen Allah ga bayinsa, domin yadda yake yalwata arziki ga wanda zai zamar masa alheri, kuma ya quntatawa wanda quntatawar ita ce alheri a gare shi.**

**3 - Haxarin fifita duniya a kan lahira.**

ذَٰلِكَ ٱلَّذِي يُبَشِّرُ ٱللَّهُ عِبَادَهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِۗ
قُل لَّآ أَسۡـَٔلُكُمۡ عَلَيۡهِ أَجۡرًا إِلَّا ٱلۡمَوَدَّةَ فِي ٱلۡقُرۡبَىٰۗ وَمَن يَقۡتَرِفۡ
حَسَنَةٗ نَّزِدۡ لَهُۥ فِيهَا حُسۡنًاۚ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٞ شَكُورٌ ٢٣ أَمۡ يَقُولُونَ
ٱفۡتَرَىٰ عَلَى ٱللَّهِ كَذِبٗاۖ فَإِن يَشَإِ ٱللَّهُ يَخۡتِمۡ عَلَىٰ قَلۡبِكَۗ وَيَمۡحُ ٱللَّهُ
ٱلۡبَٰطِلَ وَيُحِقُّ ٱلۡحَقَّ بِكَلِمَٰتِهِۦٓۚ إِنَّهُۥ عَلِيمُۢ بِذَاتِ ٱلصُّدُورِ ٢٤
وَهُوَ ٱلَّذِي يَقۡبَلُ ٱلتَّوۡبَةَ عَنۡ عِبَادِهِۦ وَيَعۡفُواْ عَنِ ٱلسَّيِّـَٔاتِ
وَيَعۡلَمُ مَا تَفۡعَلُونَ ٢٥ وَيَسۡتَجِيبُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ
ٱلصَّٰلِحَٰتِ وَيَزِيدُهُم مِّن فَضۡلِهِۦۚ وَٱلۡكَٰفِرُونَ لَهُمۡ عَذَابٞ
شَدِيدٞ ٢٦ ۞ وَلَوۡ بَسَطَ ٱللَّهُ ٱلرِّزۡقَ لِعِبَادِهِۦ لَبَغَوۡاْ فِي ٱلۡأَرۡضِ نصف الحزب ٤٩
وَلَٰكِن يُنَزِّلُ بِقَدَرٖ مَّا يَشَآءُۚ إِنَّهُۥ بِعِبَادِهِۦ خَبِيرُۢ بَصِيرٞ ٢٧ وَهُوَ
ٱلَّذِي يُنَزِّلُ ٱلۡغَيۡثَ مِنۢ بَعۡدِ مَا قَنَطُواْ وَيَنشُرُ رَحۡمَتَهُۥۚ وَهُوَ ٱلۡوَلِيُّ ٱلۡحَمِيدُ
٢٨ وَمِنۡ ءَايَٰتِهِۦ خَلۡقُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَمَا بَثَّ فِيهِمَا مِن دَآبَّةٖۚ
وَهُوَ عَلَىٰ جَمۡعِهِمۡ إِذَا يَشَآءُ قَدِيرٞ ٢٩ وَمَآ أَصَٰبَكُم مِّن مُّصِيبَةٖ فَبِمَا
كَسَبَتۡ أَيۡدِيكُمۡ وَيَعۡفُواْ عَن كَثِيرٖ ٣٠ وَمَآ أَنتُم بِمُعۡجِزِينَ
فِي ٱلۡأَرۡضِۖ وَمَا لَكُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ مِن وَلِيّٖ وَلَا نَصِيرٖ ٣١



**(23) Waccan bushara mai girma, ita ce busharar da Allah yake yi wa bayinsa, ta hannun Manzonsa ga waxanda suka yi imani da Allah da Manzanninsa, kuma suka yi ayyuka nagari. Ya kai wannan Manzo ka ce: "Ni bana neman wani lada ko sakamako a kan isar da saqo, sai sakamako xaya, wanda amfaninsa gare ku zai koma, shi ne ku so ni saboda kusancina a gare ku. Duk wanda ya aikata kyakkyawa, to zamu ninka masa ladansa, lada xaya zuwa goma. Haqiqa Allah mai yawan gafara ne ga zunuban wanda ya tuba daga cikin bayinsa, kuma mai yabawa ne ga ayyukansu nagari, wanda suke aikata su don neman yardar Allah.**

**(24) Daga abin da kafirai suke riyawa shi ne: wannan alqur'ani Annabi Muhammad ne ya qirqire shi, kuma ya danganta shi ga Ubangijinsa. Sai Allah ya mayar musu da martani, ya ce: "Da ace ranka zata riya a kan ka qirqiri qarya, da na rufe zuciyar ka ruf, kuma na goge qagen da ka yi, na bar gaskiyar. To, tunda lamarin ba haka ba ne, sai hakan ya nuna gaskiyar Annabi Muhammad (S.A.W) cewa an yi masa wahayi daga Ubangijinsa. Haqiqa Allah masani ne ga zukatan bayi, babu abin da yake vuya a gare shi.**

**(25) Shi ne (S.W.T) yake karvar tuban bayinsa daga kafirci da savo, idan sun tuba gare shi, kuma yake kauda kai ga munanan ayyukan da suka yi, kuma yana sanin duk abin da kuke aikatawa, babu abin da yake vuya a gare shi daga ayyukan ku, kuma zai yi muku sakamako a kansu.**

**(26) Kuma yana amsar roqon waxanda suka yi imani da Allah da Manzanninsa, suka yi ayyuka nagari, kuma ya qara musu da abin da basu roqa ba daga falalarsa. Waxanda suke kafirce wa Allah da Manzannisa, suna da azaba mai qarfi, da take jiransu ranar tashin alqiyama.**

**(27) Da Allah ya yalwata arziki ga bayinsa gaba xaya, da sun yi xagawa da zalunci a bayan qasa, sai dai shi (S.W.T) yana saukar da arziki gwargwadon yadda ya ga dama, na yalwatawa ko quntatawa. Haqiqa shi mai masani mai bada labari ga halin bayinsa, kuma mai gani ne, ya bayar saboda wata hikima, ko ya hana saboda wata hikima.**

**(28) Kuma shi ne wanda yake saukarwa bayinsa ruwan sama, bayan sun xebe qauna daga saukar sa, sai ya yaxa wannan ruwan sai qasa ta fitar da tsirrai, kuma shi ne yake jivintar lamarin bayinsa, kuma shi ne abin yabo a kowane hali.**

**(29) Daga cikin ayoyin Allah da suke nuna ikonsa da kaxaitakarsa, akwai: halittar sammai da halittar qassai, da abin da ya yaxa a cikinsu na halittu masu ban mamaki, kuma shi mai iko ne idan ya ga damar tara su domin yin sakayya a tsakaninsu, hakan ba zai gajiyar da shi ba kamar yadda bai gajiyar da shi ba a farkon lamari.**

**(30) Ya ku mutane , duk abin da ya same ku na musifa a kanku, ko a cikin dukiyar ku, to, sakamakon ayyukan da kuke aikatawa ne na savon Allah, kuma Allah yana yafe da yawa daga cikinsu, baya kama ku da su.**

**(31) Kuma ba zaku iya gujewa Ubangijinku ba, idan ya yi nufin yi muku uquba, kuma baku da wanda majivincin lamarin ku koma bayanku, wanda zai jivinci lamarin ku, kuma baku da wani mataimaki da ya zai xauke muku azabarsa idan ya saukar muku da ita.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyin Suke Koyarwa:

**1 - Mai kira ga Allah baya neman wani lada a wurin mutane.**

**2 - Yalwata arziki ko quntata shi yana qarqashin hikimar Allah, sai dai hikimar zata iya voyuwa ga da yawa daga cikin mutane.**

**3 - Zunubai da laifuka sune sababin faruwar musibu.**

وَمِنْ ءَايَٰتِهِ ٱلْجَوَارِ فِى ٱلْبَحْرِ كَٱلْأَعْلَٰمِ ٣٢ إِن يَشَأْ يُسْكِنِ ٱلرِّيحَ
فَيَظْلَلْنَ رَوَاكِدَ عَلَىٰ ظَهْرِهِۦٓ ۚ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَءَايَٰتٍ لِّكُلِّ صَبَّارٍ شَكُورٍ
٣٣ أَوْ يُوبِقْهُنَّ بِمَا كَسَبُوا۟ وَيَعْفُ عَن كَثِيرٍ ٣٤ وَيَعْلَمَ ٱلَّذِينَ
يُجَٰدِلُونَ فِىٓ ءَايَٰتِنَا مَا لَهُم مِّن مَّحِيصٍ ٣٥ فَمَآ أُوتِيتُم مِّن شَىْءٍ فَمَتَٰعُ
ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا ۖ وَمَا عِندَ ٱللَّهِ خَيْرٌ وَأَبْقَىٰ لِلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَلَىٰ رَبِّهِمْ
يَتَوَكَّلُونَ ٣٦ وَٱلَّذِينَ يَجْتَنِبُونَ كَبَٰٓئِرَ ٱلْإِثْمِ وَٱلْفَوَٰحِشَ وَإِذَا مَا
غَضِبُوا۟ هُمْ يَغْفِرُونَ ٣٧ وَٱلَّذِينَ ٱسْتَجَابُوا۟ لِرَبِّهِمْ وَأَقَامُوا۟ ٱلصَّلَوٰةَ
وَأَمْرُهُمْ شُورَىٰ بَيْنَهُمْ وَمِمَّا رَزَقْنَٰهُمْ يُنفِقُونَ ٣٨ وَٱلَّذِينَ إِذَآ أَصَابَهُمُ
ٱلْبَغْىُ هُمْ يَنتَصِرُونَ ٣٩ وَجَزَٰٓؤُا۟ سَيِّئَةٍ سَيِّئَةٌ مِّثْلُهَا ۖ فَمَنْ عَفَا
وَأَصْلَحَ فَأَجْرُهُۥ عَلَى ٱللَّهِ ۚ إِنَّهُۥ لَا يُحِبُّ ٱلظَّٰلِمِينَ ٤٠ وَلَمَنِ ٱنتَصَرَ
بَعْدَ ظُلْمِهِۦ فَأُو۟لَٰٓئِكَ مَا عَلَيْهِم مِّن سَبِيلٍ ٤١ إِنَّمَا ٱلسَّبِيلُ عَلَى
ٱلَّذِينَ يَظْلِمُونَ ٱلنَّاسَ وَيَبْغُونَ فِى ٱلْأَرْضِ بِغَيْرِ ٱلْحَقِّ ۚ أُو۟لَٰٓئِكَ
لَهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ ٤٢ وَلَمَن صَبَرَ وَغَفَرَ إِنَّ ذَٰلِكَ لَمِنْ عَزْمِ
ٱلْأُمُورِ ٤٣ وَمَن يُضْلِلِ ٱللَّهُ فَمَا لَهُۥ مِن وَلِىٍّ مِّنۢ بَعْدِهِۦ ۗ وَتَرَى
ٱلظَّٰلِمِينَ لَمَّا رَأَوُا۟ ٱلْعَذَابَ يَقُولُونَ هَلْ إِلَىٰ مَرَدٍّ مِّن سَبِيلٍ ٤٤



**(32) Daga cikin ayoyin Allah da suke nuna ikonsa da kaxaitakarsa, akwai: jiragen ruwa waxanda suke gudu a cikin teku tamkar duwatsu wurin girmansu da tsawonsu. (33) Idan Allah ya ga damar tsayar da iskar da take tafiyar da su, sai ya tsayar da ita, sai su yi saura tsaye cak a cikin teku basa motsi. Lallai a cikin wannan abin da aka ambata na halittar jiragen ruwa da hore iska akwai dalilai bayyanannu a kan ikon Allah, ga duk mai yawan haquri a kan bala'i da jarrabawa, mai yawan godiya ga ni'imomin Allah a gare shi.**
**(34) Ko kuma idan Allah ya ga damar ya halaka waxannan jirage ta hanyar aiko musu da iska mai qarfi, sai ya halakar da su, saboda laifukan da mutane suke aikatawa, sai dai yana yin afuwa a kan da yawa daga cikin zunuban bayinsa, baya yi musu uquba a kansu. (35) Waxanda suke jayayya a cikin ayoyin Allah don vata su, sun sani cewa yayin halakar da waxannan jirage ta hanyar aiko da iska mai qarfi, basu da wani wurin gujewa wannan halakar, don haka basa kiran kowa sai Allah, kuma suna barin duk wanda ba shi ba.**
**(36) Ya ku mutane, duk abin da aka baku na dukiya, ko matsayi, ko 'ya'ya, duk jin daxin duniya ne, kuma zai qare ya yanke, ni'ima dauwamammiya ita ce ni'imar gidan Aljannah, wadda Allah ya tanade ta ga waxanda suka yi imani da Allah da Manzanninsa, kuma ga Ubangijinsu kaxai suke dogara a cikin al'amuran su. (37) Waxanda suke nisantar manyan zunubai da munanan su, kuma idan suka yi fushi da wanda ya munana musu da magana ko aiki, sai su yafe masa kuskurensa, basa yi masa uquba a kai. Wannan afuwa karamci ne daga gare su, matuqar akwai masalaha da alheri a cikin yin hakan.**
**(38) Waxanda suka amsa kiran Ubangijinsu, ta hanyar aikata umarninsa, da barin abubuwan da ya hana, kuma suka cika sallah, da siffa mafi cika. Da waxanda suke neman shawarar juna a cikin al'amuran da suka dame su, kuma suna ciyarwa daga abin da muka azurta su da shi. (39) Waxanda idan aka cuce su, sai su rama don girmama kawunan su da samar wa kansu izza. Idan wanda ya yi zaluncin bai cancanta a yi masa afuwa ba, to wannan ramuwar daidai ce, musamman ma idan ya zama a cikin afuwar babu wata maslaha. (40) Duk wanda yake son ya bi haqqin sa, to yana da damar hakan, amma daidai yadda abin yake, ba qari ba qetare iyaka. Wanda ya yi afuwa ga wanda ya munana masa, kuma ya gyara tsakaninsa da xan uwansa, to ladansa yana wurin Allah. Haqiqa Allah baya son azzalumai, waxanda suke zaluntar mutane a dukiyarsu ko kawunansu ko mutuncinsu, kai Allah yana qinsu ma. (41) Duk wanda ya nemi haqqinsa bayan an zalunce shi, to waxannan babu wani laifi a kansu, saboda sun karvi haqqinsu. (42) Zargi da uquba suna kan waxanda suke zaluntar mutane, kuma suke savo a bayan qasa, waxannan suna da azaba mai raxaxi a lahira.**
**(43) Amma wanda ya yi haquri a kan cutar da waninsa ya yi masa, kuma ya yafe masa, to wannan alheri zai jawo masa alheri da al'ummar da yake rayuwa a cikinsu, wannan abu ne abin yabo, ba kowa ake datarwa ga haka ba sai ma'abocin babban rabo.(44) Duk wanda Allah ya tavar da shi ga barin shiriya, ya vatar da shi daga gaskiya, to wannan ba shi da wani majivincin lamari da zai jivinci lamarinsa. Kuma zaka ga waxanda suka zalunci kawunansu da kafirci, da savon Allah, yayin da suka ga azabar Allah a ranar alqiyama, suna burin, shin ko akwai wata hanya da za a koma zuwa duniya, mu tuba zuwa ga Allah.?**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Haquri da godiyar Allah sababi ne guda biyu da suke sanya izina da ayoyin Allah. 2 - Matsayin shawara a cikin musulunci yana da girma.**
**3 - Halarcin kama macuci da kwatankwacin cutar da ya yi, amma afuwa ita ta fi haka alheri.**

وَتَرَىٰهُمْ يُعْرَضُونَ عَلَيْهَا خَٰشِعِينَ مِنَ ٱلذُّلِّ يَنظُرُونَ
مِن طَرْفٍ خَفِيٍّ ۗ وَقَالَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓا۟ إِنَّ ٱلْخَٰسِرِينَ ٱلَّذِينَ
خَسِرُوٓا۟ أَنفُسَهُمْ وَأَهْلِيهِمْ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ ۗ أَلَآ إِنَّ ٱلظَّٰلِمِينَ
فِى عَذَابٍ مُّقِيمٍ ٤٥ وَمَا كَانَ لَهُم مِّنْ أَوْلِيَآءَ يَنصُرُونَهُم
مِّن دُونِ ٱللَّهِ ۗ وَمَن يُضْلِلِ ٱللَّهُ فَمَا لَهُۥ مِن سَبِيلٍ ٤٦ ٱسْتَجِيبُوا۟
لِرَبِّكُم مِّن قَبْلِ أَن يَأْتِىَ يَوْمٌ لَّا مَرَدَّ لَهُۥ مِنَ ٱللَّهِ ۚ مَا لَكُم
مِّن مَّلْجَإٍ يَوْمَئِذٍ وَمَا لَكُم مِّن نَّكِيرٍ ٤٧ فَإِنْ أَعْرَضُوا۟
فَمَآ أَرْسَلْنَٰكَ عَلَيْهِمْ حَفِيظًا ۖ إِنْ عَلَيْكَ إِلَّا ٱلْبَلَٰغُ ۗ وَإِنَّآ إِذَآ
أَذَقْنَا ٱلْإِنسَٰنَ مِنَّا رَحْمَةً فَرِحَ بِهَا ۖ وَإِن تُصِبْهُمْ سَيِّئَةٌۢ
بِمَا قَدَّمَتْ أَيْدِيهِمْ فَإِنَّ ٱلْإِنسَٰنَ كَفُورٌ ٤٨ لِّلَّهِ مُلْكُ
ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۚ يَخْلُقُ مَا يَشَآءُ ۚ يَهَبُ لِمَن يَشَآءُ إِنَٰثًا
وَيَهَبُ لِمَن يَشَآءُ ٱلذُّكُورَ ٤٩ أَوْ يُزَوِّجُهُمْ ذُكْرَانًا وَإِنَٰثًا ۖ
وَيَجْعَلُ مَن يَشَآءُ عَقِيمًا ۚ إِنَّهُۥ عَلِيمٌ قَدِيرٌ ٥٠ ۞ وَمَا كَانَ (ثلاثة أرباع الحزب ٤٩)
لِبَشَرٍ أَن يُكَلِّمَهُ ٱللَّهُ إِلَّا وَحْيًا أَوْ مِن وَرَآئِ حِجَابٍ أَوْ يُرْسِلَ
رَسُولًا فَيُوحِىَ بِإِذْنِهِۦ مَا يَشَآءُ ۚ إِنَّهُۥ عَلِىٌّ حَكِيمٌ ٥١



**(45) Ya kai wannan Manzo, zaka ga waxannan azzalumai lokacin da ake bijiro da su ga wuta, a cikin qasqanci da kunyata, suna kallon mutane a sace, saboda tsananin tsorata da azaba. Waxanda suka yi imani da Allah da Manzannnisa suka ce: "Haqiqanin waxanda suka yi asara da gaske su ne: waxanda suka yi asarar kawunansu da iyalansu a ranar alqiyama, saboda abin da suka haxu da shi daga azabar Allah. Ku saurara, haqiqa waxanda suka zalunci kansu da yin kafirci da aikata savon Allah, suna cikin azaba dauwamammiya, wadda bata yankewa.**

**(46) Kuma basu da wasu masoya da zasu taimaka, su tseratar da su daga azabar Allah ranar alqiyama. Duk wanda Allah ya tavar da shi ga barin gaskiya, ya vatar da shi, to har abad ba zai tava samun wata hanya da zata kai shi zuwa ga shiriya ba.**

**(47) Ya ku mutane, ku amsa kiran Ubangijinku ta hanyar yin gaggawa wurin kamanta umarninsa, da nisantar abubuwan da ya hana, da barin zan yi- zan yi, tun gabanin ranar alqiyama ta zo, wadda idan ta zo baku da wata mafaka, da zaku fake a cikinta, kuma baku da wani inkari da zaku yi inkarin laifukanku da kuka aikata a duniya da shi.**

**(48) Idan suka bijire daga abin da ka umarce su da shi – Ya kai wannan Manzo, to ba mu aiko ka ka zama mai tsaro a kansu ba, kana kiyaye ayyukansu, babu abin da yake kanka sai isar da saqon abin da aka umarce ka da isarwa, su kuma hisabin su yana wajen Allah. Haqiqa mu idan muka xanxanawa mutum rahama daga gare mu, kamar ta wadata, da lafiya da makamantan su, sai ya yi farin ciki da ita, amma idan wani bala'i ko abin qi ya samu mutane saboda laifukansu, to xabi'ar mutane ita ce butulci ga ni'imomin Allah, da rashin godiya a kansu, da fushi da abin da Allah ya tsara shi da hikimarsa.**

**(49) (50) Mulkin sammai da qassai duk na Allah ne, yana halittar abin da ya ga dama, na namiji ko mace, ko wanin haka, yana ba wanda ya ga dama 'ya'ya mata ya hana shi 'ya'ya maza, kuma yana ba wanda ya ga dama 'ya'ya maza, ya hana shi 'ya'ya mata, ko kuma ya haxawa wanda ya ga dama maza da mata, kuma yana sa wanda ya ga dama ya zama bakararre, baya haihuwa, haqiqa shi Allah Masani ga abin da ya faru, da wanda zai faru a nan gaba, don haka wannan yana cikin cikar iliminsa, da cikar hikimarsa, babu abin da yake vuyar masa, kuma babu abin da yake gagararsa.**

**(51) Bai inganta Allah ya yi magana da wani mutun ba sai ta hanyar wahayi, ko ilhama, ko wanin haka, ko ya yi masa magana ta yadda ba zai gan shi ba sai dai ya ji maganarsa kawai, ko kuma ya aiko masa da Manzo daga cikin Mala'iku kamar Jibrilu, sai ya yi wahayin abin da aka aiko shi da shi ga Manzo a cikin mutane, da abin da Allah ya ga dama na wahayi. Haqiqa Allah Maxaukaki ne a cikin siffarsa da zatinsa, kuma mai hikima ne a cikin halittarsa da ikonsa da shari'arsa.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Wajabcin gaggawa zuwa ga kamanta umarnin Allah, da nisantar abubuwan da ya hana.**

**2 - Aikin Manzo shi ne isar da saqo, amma sakamakon hakan yana hannun Allah.**

**3 - Kyautar 'ya'ya maza ko mata, ko duka biyun, tana faruwa ne bisa ilimin Allah da saninsa ga abin da ya dace da bayinsa, babu wata falala da 'ya'ya maza suke da ita koma bayan mata.**

**4 - Allah yana yin wahayi ga Annabawansa ta hanyoyi daban daban, saboda wasu hikimomi da shi kaxai ya san su.**

وَكَذَٰلِكَ أَوۡحَيۡنَآ إِلَيۡكَ رُوحٗا مِّنۡ أَمۡرِنَاۚ مَا كُنتَ تَدۡرِي مَا ٱلۡكِتَٰبُ
وَلَا ٱلۡإِيمَٰنُ وَلَٰكِن جَعَلۡنَٰهُ نُورٗا نَّهۡدِي بِهِۦ مَن نَّشَآءُ مِنۡ عِبَادِنَاۚ
وَإِنَّكَ لَتَهۡدِيٓ إِلَىٰ صِرَٰطٖ مُّسۡتَقِيمٖ ٥٢ صِرَٰطِ ٱللَّهِ ٱلَّذِي لَهُۥ
مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِۗ أَلَآ إِلَى ٱللَّهِ تَصِيرُ ٱلۡأُمُورُ ٥٣

سُورَةُ الزُّخۡرُفِ — ترتيبها ٤٣ — آياتها ٨٩

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

حمٓ ١ وَٱلۡكِتَٰبِ ٱلۡمُبِينِ ٢ إِنَّا جَعَلۡنَٰهُ قُرۡءَٰنًا عَرَبِيّٗا
لَّعَلَّكُمۡ تَعۡقِلُونَ ٣ وَإِنَّهُۥ فِيٓ أُمِّ ٱلۡكِتَٰبِ لَدَيۡنَا
لَعَلِيٌّ حَكِيمٌ ٤ أَفَنَضۡرِبُ عَنكُمُ ٱلذِّكۡرَ صَفۡحًا
أَن كُنتُمۡ قَوۡمٗا مُّسۡرِفِينَ ٥ وَكَمۡ أَرۡسَلۡنَا مِن نَّبِيّٖ فِي
ٱلۡأَوَّلِينَ ٦ وَمَا يَأۡتِيهِم مِّن نَّبِيٍّ إِلَّا كَانُواْ بِهِۦ يَسۡتَهۡزِءُونَ
٧ فَأَهۡلَكۡنَآ أَشَدَّ مِنۡهُم بَطۡشٗا وَمَضَىٰ مَثَلُ ٱلۡأَوَّلِينَ
٨ وَلَئِن سَأَلۡتَهُم مَّنۡ خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ لَيَقُولُنَّ
خَلَقَهُنَّ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡعَلِيمُ ٩ ٱلَّذِي جَعَلَ لَكُمُ ٱلۡأَرۡضَ
مَهۡدٗا وَجَعَلَ لَكُمۡ فِيهَا سُبُلٗا لَّعَلَّكُمۡ تَهۡتَدُونَ ١٠



**52 Kamar yadda muka yi wahayi zuwa ga Annabawa a gabaninka – Ya kai wannan Manzo - haka muka yi maka wahayin Alqur'ani daga wurinmu, gabaninsa baka san mene ne littafan da aka saukarwa Manzanni daga sama ba, kuma baka san mene ne imani ba. Sai dai mun saukar maka da wannan Alqur'ani don ya zama haske, da muke shiryar da wanda muka ga dama daga cikin bayinmu. Haqiqa kai kana nusar da mutane ga hanya miqaqqiya, ita ce addinin musulunci.**

**53 Ita ce hanyar Allah wanda yake da mulkin abin da yake cikin sammai da qassai, halittarsa ce, mulkinsa ne, tsarinsa ne. Tabbas zuwa ga Allah shi kaxai ake mayar da dukkan al'amura, wajen qaddara su da tsara su.**

# Suratuz Zukhruf

An Saukar Da Ita A Makkah

## Daga Manufofin Surar:

**Bayani a kan ingantattun ginshiqan da Alqur'ani ya zo da su, da kuma warware tunane-tunanen jahiliyya marasa kyau da tushe.**

## Tafsir:

**1 (Haa Mim) Bayani akan ire-iren waxannan haruffai ya gabata a farkon suratul Baqara.**

**2 Allah ya rantse da Alqur'ani wanda yake bayyana hanyar shiriya zuwa ga gaskiya.**

**3 Haqiqa mun sanya shi abin karantawa (Alqur'ani) da harshen larabawa, domin kwaxayin ku hankalce shi – Ya ku taron waxanda ya sauka da harshenku - ku gane ma'anoninsa, ku fahimce su, don ku isar da shi zuwa ga sauran al'ummu.**

**4 Tabbas haqiqa wannan Alqur'ani a cikin Lauhul Mahafuz ma'abocin xaukaka ne da girma, kuma ma'abocin hikima ne, an kyautata ayoyinsa wajen abubuwan da ya yi umarni da abubuwan da ya hana.**

**5 Yanzu zamu bar saukar muku da Alqur'ani, mu bada baya, saboda kawai kuna yawaita aikata shirka da savon Allah? Ba zamu aikata haka ba, domin jinqai gare ku yana hukunta savanin hakan.**

**6 Annabi nawa muka aika zuwa ga al'ummun da suka gabata (Wato suna da yawa).**

**7 Babu wani Annabi da ya je wurin waxancan al'ummu da suka gabata daga wurin Allah, face sun kasance masu yi masa izgilanci.**

**8 Sai muka halakar da al'ummun da sun fi qarfi daga cikin waxancan al'ummu, don haka ba zamu gaza halakar da waxanda suka fi su rauni ba. Siffar yadda aka halakar da al'ummun da suka wuce ya gabata A cikin Al'qur'ani, kamar su Adawa, da Samudawa, da mutanen Annabi luxu, da mutanen Madyana.**

**9 Ya kai wannan Manzo, idan ka tambayi waxannan mushirikai masu qaryatawa: "Wane ne ya halicci sammai, kuma wane ne ya halicci qassai? Tabbas zasu baka amsa da cewa: "Allah Mabuwayi wanda babu mai yin galaba a kansa, Masanin komai, shi ne ya halicce su".**

**10 Allah wanda ya shimfixa muku qasa, ya sanya ta abar takawa, kuna taka ta da qafafunku, kuma ya sanya muku hanyoyi a cikin duwatsun ta, da kwarinta, ko kwa gane hanya da ita cikin tafiye tafiyenku.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - An kira wahayi da ruhi domin muhimmancinsa wurin shiryar da mutane, kuma shi tamkar rai ne a gangar jiki.**

**2 - Shiriyar war da aka danganta ta da Manzon Allah (S.A.W) ita ce shiryarwa ta nusarwa, ba shiryarwar da datarwa ba. 3 - Tauhidin da mushirikai ke da shi na rububiyya, (Tauhidin tabbatarwa da Allah ayyukansa) ba zai amfanar da su ba a ranar alqiyama.**

وَٱلَّذِي نَزَّلَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءَۢ بِقَدَرٖ فَأَنشَرۡنَا بِهِۦ بَلۡدَةٗ مَّيۡتٗاۚ
كَذَٰلِكَ تُخۡرَجُونَ ١١ وَٱلَّذِي خَلَقَ ٱلۡأَزۡوَٰجَ كُلَّهَا وَجَعَلَ
لَكُم مِّنَ ٱلۡفُلۡكِ وَٱلۡأَنۡعَٰمِ مَا تَرۡكَبُونَ ١٢ لِتَسۡتَوُۥاْ عَلَىٰ ظُهُورِهِۦ
ثُمَّ تَذۡكُرُواْ نِعۡمَةَ رَبِّكُمۡ إِذَا ٱسۡتَوَيۡتُمۡ عَلَيۡهِ وَتَقُولُواْ سُبۡحَٰنَ
ٱلَّذِي سَخَّرَ لَنَا هَٰذَا وَمَا كُنَّا لَهُۥ مُقۡرِنِينَ ١٣ وَإِنَّآ إِلَىٰ رَبِّنَا
لَمُنقَلِبُونَ ١٤ وَجَعَلُواْ لَهُۥ مِنۡ عِبَادِهِۦ جُزۡءًاۚ إِنَّ ٱلۡإِنسَٰنَ
لَكَفُورٞ مُّبِينٌ ١٥ أَمِ ٱتَّخَذَ مِمَّا يَخۡلُقُ بَنَاتٖ وَأَصۡفَىٰكُم
بِٱلۡبَنِينَ ١٦ وَإِذَا بُشِّرَ أَحَدُهُم بِمَا ضَرَبَ لِلرَّحۡمَٰنِ مَثَلٗا
ظَلَّ وَجۡهُهُۥ مُسۡوَدّٗا وَهُوَ كَظِيمٌ ١٧ أَوَمَن يُنَشَّؤُاْ فِي
ٱلۡحِلۡيَةِ وَهُوَ فِي ٱلۡخِصَامِ غَيۡرُ مُبِينٖ ١٨ وَجَعَلُواْ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةَ
ٱلَّذِينَ هُمۡ عِبَٰدُ ٱلرَّحۡمَٰنِ إِنَٰثًاۚ أَشَهِدُواْ خَلۡقَهُمۡۚ سَتُكۡتَبُ
شَهَٰدَتُهُمۡ وَيُسۡـَٔلُونَ ١٩ وَقَالُواْ لَوۡ شَآءَ ٱلرَّحۡمَٰنُ مَا عَبَدۡنَٰهُمۗ
مَّا لَهُم بِذَٰلِكَ مِنۡ عِلۡمٍۖ إِنۡ هُمۡ إِلَّا يَخۡرُصُونَ ٢٠ أَمۡ ءَاتَيۡنَٰهُمۡ
كِتَٰبٗا مِّن قَبۡلِهِۦ فَهُم بِهِۦ مُسۡتَمۡسِكُونَ ٢١ بَلۡ قَالُوٓاْ إِنَّا
وَجَدۡنَآ ءَابَآءَنَا عَلَىٰٓ أُمَّةٖ وَإِنَّا عَلَىٰٓ ءَاثَٰرِهِم مُّهۡتَدُونَ ٢٢



**(11) Shi ne wanda ya saukar da ruwa daga sama, gwargwadon yadda zai ishe ku, kuma ya ishi dabbobinku da shukarku, kuma muka raya qasar da ta qeqashe da shi, maras tsiro, to kamar yadda Allah ya raya wannan qasar da ta qeqashe da tsiro haka ne yake raya ku don tashin alqiyama.**

**(12) Shi ne wanda ya halicci kowane irin abu, kamar dare da rana, namiji da mace da sauransu, kuma ya sanya muku jiragen ruwa da dabbobi su zama ababen hawa a gare ku, a yayin tafiye –tafiyen ku, sai ku hau jiragen ruwa a cikin teku, ku hau dabbobin ku akan tsandauri.**

**(13) Yayi muku haka ne gaba xaya, da fatan zaku tabbata a bayan ababen da kuke hawa yayin tafiye-tafiyen ku, sannan ku tuna ni'imar da Ubangijinku ya yi muku, da hore muku su gare ku, yayin da kuka daidaita a kan bayansu, sai ku faxa da harshenku cewa: "Tsarki ya tabbata ga wanda ya samar mana wannan, ya hore mana wannan abin hawa, ga shi muna sarrafa su, kuma ba don Allah ya hore mana su ba da ba zamu iya ba".**

**(14) Kuma haqiqa mu ga Ubangijinmu kaxai zamu koma, bayan mutuwar mu, domin ya yi mana hisabi da bada sakamako.**

**(15) Mushirikai sun riya cewa wai wasu daga cikin halitta an haife su ne daga Allah, yayin da suka ce: "Mala'iku 'ya'yan Allah ne mata". Haqiqa duk mutumin da yake faxar irin wannan magana, to mai yawan butulci ne da kafirci a bayyane.**

**(16) Ya ku mushirikai, yanzu kuna cewa: "Allah ya riqi 'ya'ya mata daga abin da ya halitta, ku kuma ya keve ku da 'ya'ya maza? Wannan wane irin rabo ne haka, kuke rayawa?.**

**(17) Alhali idan aka yi wa xayansu bushara da samun 'ya mace, wadda yake danganawa Ubangijinsa, sai fuskarsa ta yi baqi qirin, saboda tsananin damuwa da baqin ciki, ya zauna cike da fushi. To yaya zai danganawa Ubangijinsu abin da yake fushi da shi, idan an yi masa bushara da shi?.**

**(18) Yanzu sa riqa dangawa Ubangijin su wanda ake reno cikin ado, kuma a yayin jayayya baya iya gamsarwa da futo da zance yadda ya kamata, saboda matantaka?!.**

**(19) Kuma sun ambaci Mala'ikun Allah, waxanda bayi ne gare shi da cewa: mata ne, shin suna wurin ne lokacin da Allah ya halicce su? Suka gane su mata ne? Da sannu Mala'iku zasu rubuta wannan shaidar da suka yi, kuma a tambaye su a kanta ranar alqiyama, a azabtar da su a kan wannan qarya da suka yi.**

**(20) Suka ce, suna masu kafa hujja da qaddara: "Da Allah ya ga damar kada mu bautawa Mala'iku da ba mu bauta musu ba, kasancewar ya ga damar haka, daga gare mu, sai ya nuna ya yarda da hakan, to basu da wani ilimi a kan wannan magana, su ba kowa ba ne face maqaryata.**

**(21) Shin ko mun ba wa waxannan mushirikai wani littafi ne gabanin Alqur'ani da yake halatta musu bautar wanin Allah?!. Don haka suka yi riqo da wannan littafi, suke kafa hujja da shi.**

**(22) Ba haka ba ne, hakan bai faru ba, sun dogara da kwaikwayo ne, suka ce: "Haqiqa mun samu iyayen mu a gabanin mu a kan wani addini da wata hanya, don sun kasance suna bautawa gumaka, saboda haka mu ma zamu ci gaba a kan hanyar su, wajen bautawa gumaka.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Kowace ni'ima ta Allah tana wajabta godiya. 2 - Zaluncin mushirikai a cikin haqqin Allah Ubangijinsu, domin sun rava masa 'ya'ya mata, alhali su basa so. 3 - Vacin kafa hujja da qaddara a kan savon Allah.**
**4 - Gani xaya ne daga cikin abubuwan da ake tabbatar da gaskiya da shi.**

وَكَذَٰلِكَ مَآ أَرۡسَلۡنَا مِن قَبۡلِكَ فِي قَرۡيَةٖ مِّن نَّذِيرٍ إِلَّا قَالَ مُتۡرَفُوهَآ
إِنَّا وَجَدۡنَآ ءَابَآءَنَا عَلَىٰٓ أُمَّةٖ وَإِنَّا عَلَىٰٓ ءَاثَٰرِهِم مُّقۡتَدُونَ ٢٣
الحزب ٥٠ ۞ قَٰلَ أَوَلَوۡ جِئۡتُكُم بِأَهۡدَىٰ مِمَّا وَجَدتُّمۡ عَلَيۡهِ ءَابَآءَكُمۡۖ
قَالُوٓاْ إِنَّا بِمَآ أُرۡسِلۡتُم بِهِۦ كَٰفِرُونَ ٢٤ فَٱنتَقَمۡنَا مِنۡهُمۡۖ فَٱنظُرۡ
كَيۡفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلۡمُكَذِّبِينَ ٢٥ وَإِذۡ قَالَ إِبۡرَٰهِيمُ لِأَبِيهِ وَقَوۡمِهِۦٓ
إِنَّنِي بَرَآءٞ مِّمَّا تَعۡبُدُونَ ٢٦ إِلَّا ٱلَّذِي فَطَرَنِي فَإِنَّهُۥ سَيَهۡدِينِ
٢٧ وَجَعَلَهَا كَلِمَةَۢ بَاقِيَةٗ فِي عَقِبِهِۦ لَعَلَّهُمۡ يَرۡجِعُونَ ٢٨ بَلۡ
مَتَّعۡتُ هَٰٓؤُلَآءِ وَءَابَآءَهُمۡ حَتَّىٰ جَآءَهُمُ ٱلۡحَقُّ وَرَسُولٞ مُّبِينٞ ٢٩
وَلَمَّا جَآءَهُمُ ٱلۡحَقُّ قَالُواْ هَٰذَا سِحۡرٞ وَإِنَّا بِهِۦ كَٰفِرُونَ ٣٠ وَقَالُواْ
لَوۡلَا نُزِّلَ هَٰذَا ٱلۡقُرۡءَانُ عَلَىٰ رَجُلٖ مِّنَ ٱلۡقَرۡيَتَيۡنِ عَظِيمٍ ٣١ أَهُمۡ
يَقۡسِمُونَ رَحۡمَتَ رَبِّكَۚ نَحۡنُ قَسَمۡنَا بَيۡنَهُم مَّعِيشَتَهُمۡ فِي ٱلۡحَيَوٰةِ
ٱلدُّنۡيَاۚ وَرَفَعۡنَا بَعۡضَهُمۡ فَوۡقَ بَعۡضٖ دَرَجَٰتٖ لِّيَتَّخِذَ بَعۡضُهُم
بَعۡضٗا سُخۡرِيّٗاۗ وَرَحۡمَتُ رَبِّكَ خَيۡرٞ مِّمَّا يَجۡمَعُونَ ٣٢ وَلَوۡلَآ
أَن يَكُونَ ٱلنَّاسُ أُمَّةٗ وَٰحِدَةٗ لَّجَعَلۡنَا لِمَن يَكۡفُرُ بِٱلرَّحۡمَٰنِ
لِبُيُوتِهِمۡ سُقُفٗا مِّن فِضَّةٖ وَمَعَارِجَ عَلَيۡهَا يَظۡهَرُونَ ٣٣



**(23) Kamar yadda waxannan suka qaryata, suka kafa hujja da koyi da iyayen su, to haka nan babu wata alqarya da muka aiko musu Manzo gabaninka, face manyansu da shugabanninsu daga cikin masu arziki sun ce: “Mu mu samu iyayenmu a kan wani addini, don haka mu zamu bi hanyar su” saboda haka ba mutanen ka ba ne farau a cikin wannan abu.**

**(24) Sai Manzon su ya ce da su: “Yanzu zaku bi iyayen ku koda kuwa na zo muku da abin da ya fi addinin da suke kai alheri? Sai su ka ce: “Mu mun kafirce wa abin da aka aiko ka da shi, kai da waxanda suka rigaye ka daga cikin Manzanni”.**

**(25) Sai muka danqi al’ummun da suka qaryata Manzanni gabaninka, muka halakar da su, ka lura yaya qarshen masu qaryata Manzanninsu ya kasance, ya kasance qarshe ne mai raxaxi.**

**(26) Ya kai wannan Manzo, ka tuna lokacin da Annabi Ibrahim ya cewa babansa da mutanensa: “Tabbas ni na barranta daga abin da kuke bautawa na gumaka koma bayan Allah”.**

**(27) Sai dai Allah wanda ya halicce ni, kuma haqiqa shi ne zai shiryar da ni zuwa ga abin da yake a cikinsa akwai amfani gare ni, na bin addininsa miqaqqe.**

**(28) Annabi Ibrahim ya sanya kalmar tauhidi (la’ilaha Ilal Lahu) ta zama tabbatacciya a cikin zurriyarsa a bayansa, ba za a gushe ana samun wanda yake kaxaita Allah, kuma baya yin shirka da shi a cikinsu ba. Duk wannan ya faru ne don fatan ko zasu koma zuwa ga Allah, ta hanyar tuba zuwa ga gare shi daga shirka da savo.**

**(29) Ban gaggauta halakar da waxannan mushirikai maqaryata ba, kai! na jiyar da su daxi ne ta hanyar barin su a duniya, na kuma jiyar da iyayensu daxi a gabaninsu, har zuwa lokacin da Alqur’ani ya zo musu, da kuma Manzo mai bayani, shi ne Muhammad (S.A.W).**

**(30) Yayin da wannan Alqur’ani ya zo musu, wanda shi ne gaskiyar da babu kokwanto a cikinsa, sai suka ce: “Wannan tsafi ne, Muhammad yake yi mana, don haka mu mun kafirce da shi, ba zamu yi imani da shi ba”.**

**(31) Sai mushirikai masu qaryatawa suka ce: “Ina ma Allah ya saukar da wannan Alqur’ani ga xayan mutum biyu masu daraja a cikin garin Makkah, ko Xa’ifa? Su ne Walid xan Uqbah, da Urwatu xa Mas’ud Assaqafiy, maimakon saukar da shi ga Muhammad, talaka maraya.**

**(32) Shin su ne suke raba rahamar Ubangijinka - Ya kai wannan Manzo – su bada ita ga wanda suka ga dama, su hana ta ga wanda suka ga dama, ko kuwa Allah ne yake yin haka?. Mu ne muka raba musu arzikinsu a duniya, muka sanya mawadaci a cikinsu da talaka, don sashen su ya zama mai hidima ga sashe. Rahamar Ubangijinka a lahira ga bayinsa ta fi alheri a kan abin da waxannan suke tarawa na rayuwar duniya mai qarewa.**

**(33) Kuma ba don kada mutane su zama al’umma xaya ba a cikin kafirci, da mun sanya wa gidajen waxanda suke kafirce wa Allah rufi na azurfa, mu sanya musu matakala (ta azurfa) su riqa hawa ta kanta.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Makauniyar biyayya tana cikin dalilan vatan al’ummun da suka gabata.**
**2 - Barranta daga kafirci da kafirai dole ne.**
**3 - Raba arziki yana qarqashin hikimar Allah ne.**
**4 - Wulaqantar duniya a wurin Allah, don da tana da qimar fiffiken sauro a wajensa, da bai shayar da kafiri maqwarwa xaya ta ruwa ba.**

وَلِبُيُوتِهِمۡ أَبۡوَٰبٗا وَسُرُرًا عَلَيۡهَا يَتَّكِـُٔونَ ٣٤ وَزُخۡرُفٗاۚ وَإِن
كُلُّ ذَٰلِكَ لَمَّا مَتَٰعُ ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَاۚ وَٱلۡأٓخِرَةُ عِندَ رَبِّكَ
لِلۡمُتَّقِينَ ٣٥ وَمَن يَعۡشُ عَن ذِكۡرِ ٱلرَّحۡمَٰنِ نُقَيِّضۡ لَهُۥ شَيۡطَٰنٗا
فَهُوَ لَهُۥ قَرِينٞ ٣٦ وَإِنَّهُمۡ لَيَصُدُّونَهُمۡ عَنِ ٱلسَّبِيلِ وَيَحۡسَبُونَ
أَنَّهُم مُّهۡتَدُونَ ٣٧ حَتَّىٰٓ إِذَا جَآءَنَا قَالَ يَٰلَيۡتَ بَيۡنِي وَبَيۡنَكَ
بُعۡدَ ٱلۡمَشۡرِقَيۡنِ فَبِئۡسَ ٱلۡقَرِينُ ٣٨ وَلَن يَنفَعَكُمُ ٱلۡيَوۡمَ
إِذ ظَّلَمۡتُمۡ أَنَّكُمۡ فِي ٱلۡعَذَابِ مُشۡتَرِكُونَ ٣٩ أَفَأَنتَ تُسۡمِعُ
ٱلصُّمَّ أَوۡ تَهۡدِي ٱلۡعُمۡيَ وَمَن كَانَ فِي ضَلَٰلٖ مُّبِينٖ ٤٠ فَإِمَّا
نَذۡهَبَنَّ بِكَ فَإِنَّا مِنۡهُم مُّنتَقِمُونَ ٤١ أَوۡ نُرِيَنَّكَ ٱلَّذِي
وَعَدۡنَٰهُمۡ فَإِنَّا عَلَيۡهِم مُّقۡتَدِرُونَ ٤٢ فَٱسۡتَمۡسِكۡ بِٱلَّذِيٓ أُوحِيَ
إِلَيۡكَۖ إِنَّكَ عَلَىٰ صِرَٰطٖ مُّسۡتَقِيمٖ ٤٣ وَإِنَّهُۥ لَذِكۡرٞ لَّكَ وَلِقَوۡمِكَۖ
وَسَوۡفَ تُسۡـَٔلُونَ ٤٤ وَسۡـَٔلۡ مَنۡ أَرۡسَلۡنَا مِن قَبۡلِكَ مِن رُّسُلِنَآ
أَجَعَلۡنَا مِن دُونِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ءَالِهَةٗ يُعۡبَدُونَ ٤٥ وَلَقَدۡ أَرۡسَلۡنَا
مُوسَىٰ بِـَٔايَٰتِنَآ إِلَىٰ فِرۡعَوۡنَ وَمَلَإِيْهِۦ فَقَالَ إِنِّي رَسُولُ رَبِّ
ٱلۡعَٰلَمِينَ ٤٦ فَلَمَّا جَآءَهُم بِـَٔايَٰتِنَآ إِذَا هُم مِّنۡهَا يَضۡحَكُونَ ٤٧



**(34) Kuma mu sanyawa gidajensu qofofi, mu sanya musu gadaje, waxanda a kansu zasu riqa kishingixa, don yi musu talala da jarrabawa.**

**(35) Kuma da mun basu zinare, duk wannan ba komai ba ne face kayan jin daxin rayuwar duniya ne, amfaninsa kaxan ne, don baya dauwama. Abin da yake lahira na ni'ima shi ne ya fi alheri a wurin Ubangijinka ga masu tsoron Allah, ta hanyar kamanta abubuwan da ya umarta, da nisantar abubuwan da ya hana - Ya kai wannan Manzo.**

**(36) Duk wanda ya yi duba, ba na nutsuwa ba ga Alqur'ani, har ya kai zuwa ga bijire masa, to zamu yi masa uquba, ta hanyar xora masa shaixani, ya zalimce shi, ya ci gaba da vatar da shi.**

**(37) Lallai waxannan shaixanun da ake xora su a kan masu bijirewa Alqur'ani, suna kange su daga addinin Allah, basa kamanta abubuwan da ya umarta, basa nisantar abubuwan da ya hana, kuma suna tsammanin su shiryayyu ne a kan gaskiya, don haka basa tuba daga vatansu.**

**(38) Har lokacin da mai bijire wa ga ambaton Allah ya zo mana ranar tashin alqiyama, sai ya yi buri ya ce: "Ya kaico na, Ina ma dai tsakani na da kai - wannan shaixani - akwai tsawon dake tsakanin mahudar rana da mafaxarta, tir da kai a matsayin aboki.**

**(39) Sai Allah ya cewa kafirai ranar alqiyama: "A yau haxuwarku a cikin azaba ba zata amfane ku ba, alhali kun zalunci kawunanku da shirka da savon Allah, abokan tarayyar ku ba zasu xauke muku komai na daga azabar da kuke ciki ba".**

**(40) Haqiqa waxannan kurame ne ga barin jin gaskiya, makafi ne ga barin ganinta, to yanzu kai - wannan Manzo - zaka iya jiyar da kurma, ko shiryar da makaho, ko shiryar da wanda ya kasance cikin vata bayyananne ga barin tafarki madaidaici?.**

**(41) Kuma idan muka tafiyar da kai, ta hanyar karvar rayuwarka gabanin azabtar da su, to tabbas sai mun kama su, ta hanyar azabtar da su a rayuwar duniya da lahira, don xaukar fansa.**

**(42) Ko kuma mu nuna maka wani vangare na azabar da muka yi musu alqawarin ta. Haqiqa mu masu cikakken iko ne a kansu, baza su iya yin galaba a kanmu a cikin komai ba.**

**(43) Ya kai wannan Manzo, ka yi riqo da wahayin Ubangijinka gare ka, ka yi aiki da shi, tabbas kana kan hanyar gaskiya, wanda babu wani ruxu a cikin ta.**

**(44) Kuma tabbas wannan Alqur'ani xaukaka ce a gare ka, kuma xaukakace ga mutanenka, kuma da sannu za a tambaye ku a kan yin imani da shi ranar alqiyama, da bin shiriyarsa, da kira zuwa gare shi.**

**(45) Ya kai wannan Manzo, ka tambayi waxanda muka aiko a gabaninka daga Manzanni: "Shin mun sanya wasu ababen bauta koma bayan Allah mai rahama?!".**

**(46) Haqiqa mun aika Annabi Musa da ayoyinmu zuwa ga Fir'auna da manya-manya daga cikin mutanensa, sai ya ce da su: "Ni Manzon Ubangijin halittu ne gaba xaya".**

**(47) Yayin da ya zo musu da ayoyin mu, sai suka riqa yin dariya, saboda raini da izgilanci.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Haxarin bijirewa Alqur'ani.**

**2 - Alqur'ani xaukaka ne ga Manzon Allah (S.A.W) da mutanen sa.**

**3 - Haxuwar dukkan saqonnin Manzanni akan watsar da shirka.**

**4 - Yin izgilanci ga gaskiya siffa ce daga cikin siffofin kafirai.**

وَمَا نُرِيهِم مِّنْ ءَايَةٍ إِلَّا هِيَ أَكْبَرُ مِنْ أُخْتِهَا وَأَخَذْنَٰهُم
بِٱلْعَذَابِ لَعَلَّهُمْ يَرْجِعُونَ ﴿٤٨﴾ وَقَالُوا۟ يَٰٓأَيُّهَ ٱلسَّاحِرُ ٱدْعُ لَنَا
رَبَّكَ بِمَا عَهِدَ عِندَكَ إِنَّنَا لَمُهْتَدُونَ ﴿٤٩﴾ فَلَمَّا كَشَفْنَا
عَنْهُمُ ٱلْعَذَابَ إِذَا هُمْ يَنكُثُونَ ﴿٥٠﴾ وَنَادَىٰ فِرْعَوْنُ فِى قَوْمِهِۦ
قَالَ يَٰقَوْمِ أَلَيْسَ لِى مُلْكُ مِصْرَ وَهَٰذِهِ ٱلْأَنْهَٰرُ تَجْرِى مِن
تَحْتِىٓ أَفَلَا تُبْصِرُونَ ﴿٥١﴾ أَمْ أَنَا۠ خَيْرٌ مِّنْ هَٰذَا ٱلَّذِى هُوَ مَهِينٌ
وَلَا يَكَادُ يُبِينُ ﴿٥٢﴾ فَلَوْلَآ أُلْقِىَ عَلَيْهِ أَسْوِرَةٌ مِّن ذَهَبٍ أَوْ جَآءَ
مَعَهُ ٱلْمَلَٰٓئِكَةُ مُقْتَرِنِينَ ﴿٥٣﴾ فَٱسْتَخَفَّ قَوْمَهُۥ
فَأَطَاعُوهُ إِنَّهُمْ كَانُوا۟ قَوْمًا فَٰسِقِينَ ﴿٥٤﴾ فَلَمَّآ ءَاسَفُونَا
ٱنتَقَمْنَا مِنْهُمْ فَأَغْرَقْنَٰهُمْ أَجْمَعِينَ ﴿٥٥﴾ فَجَعَلْنَٰهُمْ
ربع الحزب ٥٠ سَلَفًا وَمَثَلًا لِّلْءَاخِرِينَ ﴿٥٦﴾ ۞ وَلَمَّا ضُرِبَ ٱبْنُ مَرْيَمَ مَثَلًا
إِذَا قَوْمُكَ مِنْهُ يَصِدُّونَ ﴿٥٧﴾ وَقَالُوٓا۟ ءَأَٰلِهَتُنَا خَيْرٌ أَمْ
هُوَ مَا ضَرَبُوهُ لَكَ إِلَّا جَدَلًۢا بَلْ هُمْ قَوْمٌ خَصِمُونَ ﴿٥٨﴾ إِنْ هُوَ
إِلَّا عَبْدٌ أَنْعَمْنَا عَلَيْهِ وَجَعَلْنَٰهُ مَثَلًا لِّبَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ ﴿٥٩﴾
وَلَوْ نَشَآءُ لَجَعَلْنَا مِنكُم مَّلَٰٓئِكَةً فِى ٱلْأَرْضِ يَخْلُفُونَ ﴿٦٠﴾



**(48) Kuma babu wata hujja da muke nunawa Fir'auna da manyan mutanensa a kan ingancin abin da Annabi Musa ya zo da shi, face sai ta fi hujjar dake gabaninta girma, kuma muka kama su da azaba a nan duniya, ko sa bar abin da suke kai na kafirci, amma ba a samu wata fa'ida ba.**

**(49) Bayan wani vangare na azaba ya same su, sai suka cewa Annabi Musa: "Ya kai wannan matsafi, ka roqa mana Ubangijinka saboda alqawarin da ya yi maka na yaye mana azaba idan muka yi imani, tabbas mu masu shiriya ne gare shi, matuqar ya yaye mana".**

**(50) Yayin da muka kawar musu da azabar, sai ga shi suna warware alqawarin su, basu cika shi ba.**

**(51) Fir'auna ya yi kira a cikin mutanensa – yana mai ji da mulkinsa – ya ce: "Ya ku mutanena, mulkin qasar misra ba nawa ba ne, kuma wannan qoramu na Nilu ba a qarqashin gidan sarautata suke gudana ba? Shin ba ku ganin mulkina ne, ku san girmana da xaukaka ta?!.**

**(52) Ni na fi Musa korarre rarrauna alheri, wanda baya iya kyautata magana.**

**(53) Ina ma Allah da ya aiko shi ya jefo masa awarwaron gwal, don bayyana cewa shi Manzonsa ne, ko Mala'iku su zo tare da shi, sashensu yana bin sashe.**

**(54) Sai Fir'auna ya ruxi mutanensa, sai suka bi shi a cikin vatansa. Haqiqa sun kasance mutane masu fita daga xa'ar Allah.**

**(55) Yayi da suka fusata mu da zarcewar su a kan kafirci sai muka damqe su, muka nutsar da su gaba xaya.**

**(56) Muka sanya Fir'auna da mutanensa suka zama a kan gaba, suna jagorantar mutane, kafiran mutanenka suna bin gurbin su a baya. muka sanya su izina ga mai wa'azantuwa, don kada ya yi irin aikinsu, sai abin da ya same su, ya same shi.**

**(57) Yayin da mushirikai suka yi zaton Annabi Isa, wanda Nasara suka bautawa shi ma ya shiga qarqashin faxin Allah: (Haqiqa ku da abin da kuke bautawa koma bayan Allah qiraren wutar Jahannama ne zaku shige ta). Kuma Allah ya hana a bauta masa, kamar yadda ya hana a bautawa gumaka, sai mutanan ka - Ya kai wannan Manzo – suka yi ihu da hayaniya cikin jayayya suka ce: "Mun yarda allolin mu su zama kamar matsayin Isa". Sai Allah ya mayar musu da martani, ya ce: "Tabbas waxanda makoma kyakkyawa ta riga ta tabbata a gare su daga wajen mu, to waxannan ababen nisantarwa daga gare ta) Wato wutar Jahannama.**

**(58) Suka ce: "Ababen bautar mu ne suka fi alheri ko kuwa Isa ne?" Xan ziba'ara da makamantansa basu buga maka wannan misali, don suna son isa ga gaskiya ba, kawai sai don son jayayya, su mutane ne da aka halicce su a kan yin husuma da jayayya.**

**(59) Annabi Isa xan Maryam ba kowa ba ne illa bawa daga cikin bayin Allah, kuma mun yi masa ni'ima da Annabta da Manzanci, kuma muka sanya shi abin buga misali ga bani-Isra'ila, suna kafa hujja da shi a kan cikar ikon Allah, yayin da ya halicce shi ba tare da uba ba, kamar yadda ya halicci Annabi Adamu ba tare da uwa da uba ba.**

**(60) Kuma da mun so mu halakar da ku – Ya ku 'ya'yan Adamu - da tuni mun halakar da ku, mu sanya Mala'iku su maye muku baya a bayan qasa, suna bautawa Allah ba tare da yin shirka da shi ba.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Warware alqawari yana cikin siffofin kafirai.**
**2 - Fasiqi hankalinsa ragagge ne, duk wanda yake son raina masa hankali, sai ya raina masa.**
**3 - Fushin Allah yana janyo asara ga bawa.**
**4 - Vatattu suna qoqarin canza manufofin nassin Alqur'ani, domin ya dace da son zuciyarsu.**

وَإِنَّهُۥ لَعِلْمٌ لِّلسَّاعَةِ فَلَا تَمْتَرُنَّ بِهَا وَٱتَّبِعُونِ ۚ هَٰذَا صِرَٰطٌ
مُّسْتَقِيمٌ ٦١ وَلَا يَصُدَّنَّكُمُ ٱلشَّيْطَٰنُ ۖ إِنَّهُۥ لَكُمْ عَدُوٌّ مُّبِينٌ
٦٢ وَلَمَّا جَآءَ عِيسَىٰ بِٱلْبَيِّنَٰتِ قَالَ قَدْ جِئْتُكُم بِٱلْحِكْمَةِ
وَلِأُبَيِّنَ لَكُم بَعْضَ ٱلَّذِى تَخْتَلِفُونَ فِيهِ ۖ فَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ وَأَطِيعُونِ
٦٣ إِنَّ ٱللَّهَ هُوَ رَبِّى وَرَبُّكُمْ فَٱعْبُدُوهُ ۚ هَٰذَا صِرَٰطٌ مُّسْتَقِيمٌ
٦٤ فَٱخْتَلَفَ ٱلْأَحْزَابُ مِنۢ بَيْنِهِمْ ۖ فَوَيْلٌ لِّلَّذِينَ ظَلَمُوا۟
مِنْ عَذَابِ يَوْمٍ أَلِيمٍ ٦٥ هَلْ يَنظُرُونَ إِلَّا ٱلسَّاعَةَ أَن
تَأْتِيَهُم بَغْتَةً وَهُمْ لَا يَشْعُرُونَ ٦٦ ٱلْأَخِلَّآءُ يَوْمَئِذٍۭ
بَعْضُهُمْ لِبَعْضٍ عَدُوٌّ إِلَّا ٱلْمُتَّقِينَ ٦٧ يَٰعِبَادِ لَا خَوْفٌ
عَلَيْكُمُ ٱلْيَوْمَ وَلَآ أَنتُمْ تَحْزَنُونَ ٦٨ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ بِـَٔايَٰتِنَا
وَكَانُوا۟ مُسْلِمِينَ ٦٩ ٱدْخُلُوا۟ ٱلْجَنَّةَ أَنتُمْ وَأَزْوَٰجُكُمْ
تُحْبَرُونَ ٧٠ يُطَافُ عَلَيْهِم بِصِحَافٍ مِّن ذَهَبٍ وَأَكْوَابٍ ۖ
وَفِيهَا مَا تَشْتَهِيهِ ٱلْأَنفُسُ وَتَلَذُّ ٱلْأَعْيُنُ ۖ وَأَنتُمْ فِيهَا
خَٰلِدُونَ ٧١ وَتِلْكَ ٱلْجَنَّةُ ٱلَّتِىٓ أُورِثْتُمُوهَا بِمَا كُنتُمْ
تَعْمَلُونَ ٧٢ لَكُمْ فِيهَا فَٰكِهَةٌ كَثِيرَةٌ مِّنْهَا تَأْكُلُونَ ٧٣



**(61) Haqiqa Annabi Isa wata alama ce daga cikin alamomin tashin alqiyama manya, lokacin da zai sauko a qarshen zamani, don haka kada ku yi shakka alqiyama zata faru, ku yi min biyayya cikin abin da na zo da shi daga wajen Allah, wannan abin da na zo muku da shi shi ne tafarki miqaqqe, wanda babu karkacewa a cikinsa.**

**(62) Kuma kada shaixan ya kautar da ku daga tafarki miqaqqe, ta hanyar ruxarku da vatarwar sa. Haqiqa shi maqiyi ne a gare ku, mai bayyana adawa.**

**(63) Yayin da Annabi Isa (A.S) ya zo wa mutanensa da dalilai bayyanannu a kan cewa shi Manzo ne, sai ya ce da su: "Haqiqa na zo muku da hikima daga wajen Allah, kuma saboda na bayyana muku wani vangare da kuka kasance kuna yin savani a kai cikin lamarin addininku, don haka ku ji tsoron Allah ta hanyar kamanta umarninsa, da nisantar abubuwan da ya hana, ku yi min xa'a cikin abin da nake umartar ku, da abin da nake hana ku.**

**(64) Haqiqa Allah shi ne Ubangijina kuma Ubangijinku, bamu da wani Ubangiji wanda ba shi ba, ku tsarkake ibada gare shi, shi kaxai. Wannan kaxaita Allan shi ne tafarki miqaqqe, wanda babu karkata a cikinsa.**

**(65) Sai qungiyoyin Nasara suka yi savani game da Annabi Isa, daga cikinsu akwai waxanda suke cewa: shi Allah ne, da waxanda suke cewa: Shi xan Allah ne. Da cikinsu akwai waxanda suke cewa: "Shi da mahaifiyarsa Alloli ne. Azaba ta tabbata ga waxanda suka zalunci kansu – ta hanyar abin da suka siffanta Annabi Isa da shi na Allantaka ko na cewa shi xan Allah ne, ko xayan uku ne - azaba mai raxaxi da take jiransu ranar alqiyama.**

**(66) Shin waxannan qungiyoyi masu savani game da Annabi Isa ba komai suke jira ba face alqiyama ta shammace su, ba tare da sun san da zuwan ta ba?!. Idan ta zo musu suna kan kafircinsu, tabbas makomarsu azaba ce mai raxaxi.**

**(67) Abokai da waxanda suka haxu a kan kafirci da vata, sashensu maqiya sashe ne ranar alqiyama, sai masu tsoron Allah, ta hanyar kamanta umarninsa, da nisantar abubuwan da ya hana, abotarsu dauwamammiya ce bata yankewa.**

**(68) Kuma Allah zai ce musu: "Ya ku bayina, a yau baku da wani tsoro cikin abin da kuke fuskanta, kuma ba zaku yi baqin ciki ba game da abin da ya kuvuce muku na rabon duniya".**

**(69) Su ne waxanda suka yi imani da Alqur'ani da aka saukarwa Manzonsu, kuma suka kasance suna jayuwa ga Alqur'ani, suna bin umarninsa, suna hanuwa daga abin da ya hana.**

**(70) Ku shiga gidan Aljannah, da ku da ire-irenku masu imani, ku yi farin ciki da abin da zaku haxu da shi na ni'ima dauwamammiya, wadda bata qarewa, kuma bata yankewa.**

**(71) Masu yi musu hidima suna kewaya su da wani mazubi na zinare, da kofuna, A cikin Aljannah akwai duk abin da rai take sha'awa, idanu suke jin daxi da ganinsa. Za ku zauna a cikinta, ba zaku fita ba har abada.**

**(72) Waccan Aljannah da aka siffata muku, ita ce wadda Allah ya gadar muku da ita saboda ayyukan ku daga falalarsa.**

**(73) Kuna da kayan marmari masu yawa a cikinta, basa yankewa, kuma daga gare su ne zaku riqa ci.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Saukar Annabi Isa alama ce babba daga cikin alamomin tashin alqiyama. 2 - Yankewar abotar fasiqai a ranar alqyama, da kuma dauwamar abotar masu tsoron Allah. 3 - Busharar Allah ga Muminai, da basu nutsuwa game da abin da suka bari a bayansu a duniya, da kuma abin da suke fuskanta a lahira.**

إِنَّ ٱلۡمُجۡرِمِينَ فِي عَذَابِ جَهَنَّمَ خَٰلِدُونَ ٧٤ لَا يُفَتَّرُ عَنۡهُمۡ وَهُمۡ
فِيهِ مُبۡلِسُونَ ٧٥ وَمَا ظَلَمۡنَٰهُمۡ وَلَٰكِن كَانُواْ هُمُ ٱلظَّٰلِمِينَ ٧٦
وَنَادَوۡاْ يَٰمَٰلِكُ لِيَقۡضِ عَلَيۡنَا رَبُّكَۖ قَالَ إِنَّكُم مَّٰكِثُونَ ٧٧ لَقَدۡ
جِئۡنَٰكُم بِٱلۡحَقِّ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَكُمۡ لِلۡحَقِّ كَٰرِهُونَ ٧٨ أَمۡ أَبۡرَمُوٓاْ أَمۡرٗا
فَإِنَّا مُبۡرِمُونَ ٧٩ أَمۡ يَحۡسَبُونَ أَنَّا لَا نَسۡمَعُ سِرَّهُمۡ وَنَجۡوَىٰهُمۚ بَلَىٰ
وَرُسُلُنَا لَدَيۡهِمۡ يَكۡتُبُونَ ٨٠ قُلۡ إِن كَانَ لِلرَّحۡمَٰنِ وَلَدٞ فَأَنَا۠ أَوَّلُ
ٱلۡعَٰبِدِينَ ٨١ سُبۡحَٰنَ رَبِّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ رَبِّ ٱلۡعَرۡشِ
عَمَّا يَصِفُونَ ٨٢ فَذَرۡهُمۡ يَخُوضُواْ وَيَلۡعَبُواْ حَتَّىٰ يُلَٰقُواْ يَوۡمَهُمُ
ٱلَّذِي يُوعَدُونَ ٨٣ وَهُوَ ٱلَّذِي فِي ٱلسَّمَآءِ إِلَٰهٞ وَفِي ٱلۡأَرۡضِ
إِلَٰهٞۚ وَهُوَ ٱلۡحَكِيمُ ٱلۡعَلِيمُ ٨٤ وَتَبَارَكَ ٱلَّذِي لَهُۥ مُلۡكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلۡأَرۡضِ وَمَا بَيۡنَهُمَا وَعِندَهُۥ عِلۡمُ ٱلسَّاعَةِ وَإِلَيۡهِ تُرۡجَعُونَ
٨٥ وَلَا يَمۡلِكُ ٱلَّذِينَ يَدۡعُونَ مِن دُونِهِ ٱلشَّفَٰعَةَ إِلَّا
مَن شَهِدَ بِٱلۡحَقِّ وَهُمۡ يَعۡلَمُونَ ٨٦ وَلَئِن سَأَلۡتَهُم مَّنۡ خَلَقَهُمۡ
لَيَقُولُنَّ ٱللَّهُۖ فَأَنَّىٰ يُؤۡفَكُونَ ٨٧ وَقِيلِهِۦ يَٰرَبِّ إِنَّ هَٰٓؤُلَآءِ قَوۡمٞ
لَّا يُؤۡمِنُونَ ٨٨ فَٱصۡفَحۡ عَنۡهُمۡ وَقُلۡ سَلَٰمٞۚ فَسَوۡفَ يَعۡلَمُونَ ٨٩



**Yayin da Allah ya ambaci sakamakon masu tsoronsa, sai ya ambaci sakamakon waxanda suke kishiyoyin su, sune masu laifi, ya ce:**

**74 Haqiqa masu laifi ta hanyar kafirci da savon Allah suna cikin azabar Jahannama ranar alqiyama, suna masu dauwama a cikinta har abada.**

**75 Ba za a rangwanta musu azaba ba, kuma su a cikinta masu yanke qauna ne daga rahamar Allah.**

**76 Ba mu zalunce su ba yayin da muka shigar da su wuta, sai dai su ne suka zalunci kawunansu da yin kafirci.**

**77 Suka kirawo Maliku mai tsaron wuta, suka ce: "Ya Maliku, Ubangijinka ya kashe mu, don mu huta da azaba". Sai Maliku ya amsa musu da cewa: "Ai ku masu zama ne a cikin azaba har abada, ba zaku mutu ba, kuma azabar ba zata yanke a kanku ba".**

**78 Haqiqa mun zo muku da gaskiya a duniya, gaskiyar da babu kokwanto a cikinta, amma da yawa daga cikinku basa son gaskiyar.**

**79 Idan sun qulla makirci ga Annabi (S.A.W) suka yi masa tanadin makirci, to mu qwararrun musu shiri ne a kansu sama da makircinsu.**

**80 Ko suna tsammanin bama jin sirrinsu ne, wanda suka voye a zukatansu?, Ko sirrin da suke ganawa da shi a boye?. Ba haka ba ne, muna jin komai gaba xaya, kuma akwai Mala'iku a tare da su suna rubuta duk abin da suka aikata.**

**81 Ya kai wannan Manzo, ka cewa waxanda suke danganawa Allah 'ya'ya mata - Allah ya xaukaka ga barin maganganunsu, xaukaka mai girma - ka ce musu: "Idan da zamu qaddara Allah yana da xa, to ni ne farkon mai bautawa wannan xan". 82 Ubangijin sammai da qassai da Al'arshi ya tsarkaka daga abin da waxannan mushirikai suke faxa na dangana masa abokin tarayya da mata da xa.**

**83 Ya kai wannan Manzo, ka rabu da su su ci gaba da kutsawa cikin abin da suke kai na vata, su yi wasa, har su haxu da ranar da ake yi musu alqawarin zuwan ta, ita ce ranar alqiyama.**

**84 Tsarki ya tabbata a gare shi shi ne abin bauta da gaskiya a sama, kuma shi ne abin bauta da gaskiya a qasa, kuma shi ne mai hikima cikin halittarsa, da gudanarwar sa, da tsarinsa, Masanin halin bayinsa, babu wani abu da yake vuya a gare shi.**

**85 Alherin Allah da albarkarsa sun qaru, wanda yake da mulkin sammai da mulkin qassai, da abin da yake tsakaninsu, kuma shi kaxai ya san lokacin da alqiyama zata tashi a cikinsa, ba wanda ya sani ba shi ba, kuma gare shi, shi kaxai zaku koma a lahira domin hisabi da bada sakamako.**

**86 Waxanda mushirikai suke bautawa koma bayan Allah basa mallakar ceto a wurin Allah, sai dai fa wanda ya shaida babu abin bautawa da gaskiya sai Allah, kuma ya san ma'anar abin da ya shaida da shi, kamar Annabi Isa da Uzairu da Mala'iku. 87 Idan da zaka tambaye su: "Wane ne ya halicce ku?" Tabbas zasu ce: "Allah ne ya halicce mu". To ta yaya ake kautar da su daga barin bautarsa bayan wannan shaidar ta su?!.**

**88 Kukan da Manzo yake kaiwa na qaryata shi da ake yi, duk Allah ya sani, da faxinsa: "Ya ubangiji, waxannan mutane sun qi yin imani da abin da ka aiko ni da shi gare su".**

**89 Ka rabu da su, ka faxi abin da zaka kuvuta daga sharrinsu - wannan a Makkah ne -. Da sannu zasu san abin da zasu haxu da shi na uquba.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Qin gaskiya yana da haxari mai girma. 2 - Makircin kafirai yana komawa kansu, koda kuwa bayan wani lokaci ne. 3 - Duk lokacin da ilimin bawa ya qaru game da Ubangijinsa, sai ya qara sakankancewa da shi, da sallamawa shari'arsa.**
**4 - Kevantuwar Allah da sanin lokacin tashin alqiyama.**

# Suratud Dukhan

An Saukar Da Ita A Makkah

سُورَةُ الدُّخَانِ — آياتها ٥٩ — ترتيبها ٤٤

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

حمٓ ١ وَٱلۡكِتَٰبِ ٱلۡمُبِينِ ٢ إِنَّآ أَنزَلۡنَٰهُ فِي لَيۡلَةٖ مُّبَٰرَكَةٍۚ
إِنَّا كُنَّا مُنذِرِينَ ٣ فِيهَا يُفۡرَقُ كُلُّ أَمۡرٍ حَكِيمٍ ٤ أَمۡرٗا
مِّنۡ عِندِنَآۚ إِنَّا كُنَّا مُرۡسِلِينَ ٥ رَحۡمَةٗ مِّن رَّبِّكَۚ إِنَّهُۥ هُوَ
ٱلسَّمِيعُ ٱلۡعَلِيمُ ٦ رَبِّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَمَا بَيۡنَهُمَآۖ
إِن كُنتُم مُّوقِنِينَ ٧ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ يُحۡيِۦ وَيُمِيتُۖ رَبُّكُمۡ
وَرَبُّ ءَابَآئِكُمُ ٱلۡأَوَّلِينَ ٨ بَلۡ هُمۡ فِي شَكّٖ يَلۡعَبُونَ ٩
فَٱرۡتَقِبۡ يَوۡمَ تَأۡتِي ٱلسَّمَآءُ بِدُخَانٖ مُّبِينٖ ١٠ يَغۡشَى ٱلنَّاسَۖ
هَٰذَا عَذَابٌ أَلِيمٞ ١١ رَّبَّنَا ٱكۡشِفۡ عَنَّا ٱلۡعَذَابَ إِنَّا مُؤۡمِنُونَ
١٢ أَنَّىٰ لَهُمُ ٱلذِّكۡرَىٰ وَقَدۡ جَآءَهُمۡ رَسُولٞ مُّبِينٞ ١٣ ثُمَّ
تَوَلَّوۡاْ عَنۡهُ وَقَالُواْ مُعَلَّمٞ مَّجۡنُونٌ ١٤ إِنَّا كَاشِفُواْ ٱلۡعَذَابِ قَلِيلًاۚ
إِنَّكُمۡ عَآئِدُونَ ١٥ يَوۡمَ نَبۡطِشُ ٱلۡبَطۡشَةَ ٱلۡكُبۡرَىٰٓ إِنَّا مُنتَقِمُونَ
نصف الحزب ٥٠ — ١٦ ۞ وَلَقَدۡ فَتَنَّا قَبۡلَهُمۡ قَوۡمَ فِرۡعَوۡنَ وَجَآءَهُمۡ رَسُولٞ كَرِيمٌ
١٧ أَنۡ أَدُّوٓاْ إِلَيَّ عِبَادَ ٱللَّهِۖ إِنِّي لَكُمۡ رَسُولٌ أَمِينٞ ١٨



**Daga Manufofin Surar: Yin gargaxi da azabar da ake jira, ta hanyar tsoratar da masu qaryatawa da azabar duniya da lahira.**

## Tafsir:

**(1) (Haa mim) Bayani a kan ire-iren waxannan haruffa ya gabata a farkon suratul Baqara.**

**(2) Allah ya rantse da Alqur'ani mai shiryarwa zuwa ga tafarkin shiriya da gaskiya. (3) Haqiqa mun saukar da Alqur'ani a cikin daren lailatul Qadri, shi wani dare ne mai yawan alherai, kuma haqiqa mu, mun kasance masu tsoratarwa da wannan Alqur'ani. (4) A wannan dare ne ake rarrabe dukkan wani lamari da aka hukunta, wanda yake da alaqa da arzikin bayi da ajalinsu, da wanin hakan, daga cikin abin da Allah zai farar a cikin wannan shekara. (5) Muna rarrabe kowane al'amari mai cike da hikima daga wajen mu. Haqiqa mu, mu ne masu aiko da Manzanni.**

**(6) Ya kai wannan Manzo, Muna aiko da Manzanni don jin qai daga Ubangijinka ga waxanda aka aiko musu da shi. Haqiqa Allah mai jin maganganun bayinsa ne, masani ayyukansu da niyyoyinsu, babu wani abin da yake vuya a gare shi daga cikinsu. (7) Ubangijin sammai, kuma Ubangijin qassai, kuma Ubangijin abin da yake tsakaninsu, idan har kun sakankance da haka, to ku yi imani da Manzannina. (8) Babu wani abin bautawa da gaskiya wanda ba shi ba, yana rayawa kuma yana kashewa, babu mai rayawa, babu mai kashewa wanda ba shi ba, Ubangijinku kuma Ubangijin iyayenku magabata.**

**(9) Sai dai waxannan mushirikai basu sakankance da hakan ba, suna cikin shakka a kan haka, suna ta yin wasanninsu, saboda vatan da suke kai. (10) Ya kai wannan Manzo ka jira azabar mutanenka a kurkusa, ranar da sama zata zo da wani hayaqi bayyananne, zasu gan shi da idanuwansu saboda tsananin azaba.**

**(11) Zai game mutanenka, kuma za a ce da su: "Wannan azabar da ta same ku, azaba ce mai ciwo".**

**(12) Sai su qasqantar da kansu ga Ubangijinsu suna roqonsa: "Ya Ubangijin mu ka yaye mana azabar da ka aiko mana, haqiqa zamu yi imani da kai da Manzonka matuqar ka yaye mana".**

**(13) To ta yaya ma zasu tuna, su koma ga Ubangijinsu, alhali Manzo mai bayyanannen saqo ya zo musu, kuma sun san gaskiyarsa, da amanarsa?! (14) Amma sai suka bijire ga barin gasgata shi, suka ce game da shi: "Koya masa ake yi, wani ne yake koya masa, ba Manzo ba ne" suka ce: "Mahaukaci ne".**

**(15) Haqiqa mu a yayin da muka kawar muku da azaba wani xan lokaci kaxan, ku masu komawa ne zuwa ga kafircin ku da qaryatawar ku. (16) Ya kai wannan Manzo, ka jira su, lokacin da zamu damqi kafirai cikin mutanenka babbar damqa, ranar yaqin Badar, tabbas mu masu xaukar fansa ne a kansu, saboda kafircewarsu ga Allah, da qaryata Manzonsa. (17) Kuma haqiqa mun jarrabi mutanen Fir'auna a gabaninsu, kuma wani Manzo mai girma ya zo musu daga Allah, yana kiran su zuwa ga kaxaita Allah da bautarsa, shi ne Annabi Musa (A.S).**

**(18) Annabi Musa ya cewa Fir'auna da mutanensa: ku bar min banu-Isra'ila, su bayin Allah ne, baku da wani haqqi na bautar da su, ni Manzo ne zuwa gare ku daga Allah, kuma amintacce a cikin abin da ya umarce ni in isar muku, ba zan rage komai ba, kuma ba zan qara ba".**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Saukar Alqur'ani a daren lailatul qadri, wanda dare ne mai yawan alheri, yana nuna girman daren.**

**2 - Aiko da Manzanni, da saukar da Alqur'ani, suna daga cikin alamomin da suke nuna rahamar Allah ga bayinsa.**

**3 - Saqon Annabawa 'yantar da raunana ne daga damqar masu girman kai.**

وَأَن لَّا تَعْلُوا عَلَى اللَّهِ ۖ إِنِّي آتِيكُم بِسُلْطَانٍ مُّبِينٍ ١٩ وَإِنِّي عُذْتُ
بِرَبِّي وَرَبِّكُمْ أَن تَرْجُمُونِ ٢٠ وَإِن لَّمْ تُؤْمِنُوا لِي فَاعْتَزِلُونِ ٢١
فَدَعَا رَبَّهُ أَنَّ هَٰؤُلَاءِ قَوْمٌ مُّجْرِمُونَ ٢٢ فَأَسْرِ بِعِبَادِي لَيْلًا إِنَّكُم
مُّتَّبَعُونَ ٢٣ وَاتْرُكِ الْبَحْرَ رَهْوًا ۖ إِنَّهُمْ جُندٌ مُّغْرَقُونَ ٢٤ كَمْ
تَرَكُوا مِن جَنَّاتٍ وَعُيُونٍ ٢٥ وَزُرُوعٍ وَمَقَامٍ كَرِيمٍ ٢٦ وَنَعْمَةٍ
كَانُوا فِيهَا فَاكِهِينَ ٢٧ كَذَٰلِكَ ۖ وَأَوْرَثْنَاهَا قَوْمًا آخَرِينَ ٢٨ فَمَا
بَكَتْ عَلَيْهِمُ السَّمَاءُ وَالْأَرْضُ وَمَا كَانُوا مُنظَرِينَ ٢٩ وَلَقَدْ
نَجَّيْنَا بَنِي إِسْرَائِيلَ مِنَ الْعَذَابِ الْمُهِينِ ٣٠ مِن فِرْعَوْنَ ۚ إِنَّهُ
كَانَ عَالِيًا مِّنَ الْمُسْرِفِينَ ٣١ وَلَقَدِ اخْتَرْنَاهُمْ عَلَىٰ عِلْمٍ عَلَى
الْعَالَمِينَ ٣٢ وَآتَيْنَاهُم مِّنَ الْآيَاتِ مَا فِيهِ بَلَاءٌ مُّبِينٌ ٣٣
إِنَّ هَٰؤُلَاءِ لَيَقُولُونَ ٣٤ إِنْ هِيَ إِلَّا مَوْتَتُنَا الْأُولَىٰ وَمَا نَحْنُ
بِمُنشَرِينَ ٣٥ فَأْتُوا بِآبَائِنَا إِن كُنتُمْ صَادِقِينَ ٣٦ أَهُمْ
خَيْرٌ أَمْ قَوْمُ تُبَّعٍ وَالَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْ ۚ أَهْلَكْنَاهُمْ ۖ إِنَّهُمْ كَانُوا
مُجْرِمِينَ ٣٧ وَمَا خَلَقْنَا السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضَ وَمَا بَيْنَهُمَا لَاعِبِينَ
٣٨ مَا خَلَقْنَاهُمَا إِلَّا بِالْحَقِّ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ٣٩



**(19) Kuma kada ku yi wa Allah girman kai, ta hanyar barin bautar sa, da yi wa bayinsa girman kai, haqiqa ni zan zo muku da hujja bayyananniya.**
**(20) Kuma ni na yi riqo da Ubangiji na, kuma Ubangijinku, kada ku kashe ni ta hanyar jefewa da duwatsu.**
**(21) Idan baku gasgata ni cikin abin da na zo muku da shi ba, to ku rabu da ni, kada ku kusance ni da cutarwa.**
**(22) Sai Annabi Musa (A.S) ya roqi Ubangijinsa, yana mai cewa: "Waxannan mutane - Fir'auna da mutanensa - masu laifi ne, sun cancanci a gaggauto musu da azaba".**
**(23) Sai Allah ya umarci Annabi Musa (A.S) da ya tafi da mutanensa a cikin dare, kuma ya ba shi labarin cewa, Fir'auna da mutanensa zasu biyo bayansu.**
**(24) Kuma ya umarce shi idan ya tsallake teku, shi da mutanensa banu Isra'il ya bar tekun a tsaye, kamar yadda yake. Haqiqa Fir'auna da rundunarsa ababen halakarwa ne ta hanyar nutsar da su a cikin teku.**
**(25) Fir'auna da mutanensa sun bar lambuna da gonaki, da qoramu masu gudana da yawa.**
**(26) Haka nan sun bar shuke-shueke da wuraren zama masu kyau masu tarin yawa!.**
**(27) Kuma sun bar rayuwa a bayansu ta jin daxi matuqa!.**
**(28) Yadda aka siffanta muku, to haka ya faru gare su, kuma muka gadar da gonakinsu, da qoramunsu, da shuke-shukensu, da wuraren zamansu ga wasu mutanen daban, su ne bani -Isra'ila.**
**(29) Sama da qasa basu yi kuka ba, yayin da Fir'auna da mutanensa suka nutse a cikin teku, kuma ba a jinkirta musu ba, ballantana su tuba. (30) Haqiqa mun tseratar da bani-Isra'ila daga azaba ta qasqanci, ta yadda Fir'auna da mutanensa suka kasance suna kashe musu 'ya'yansu maza, suna qyale 'ya'yansu mata.**
**(31) Mun ceto su daga azabar Fir'auna, tabbas ya kasance mai girman kai, kuma mai wuce iyaka cikin lamarin Allah da addininsa. (32) Haqiqa mun zavi bani-isra'ila bisa ga ilimi, a kan mutanen zamaninsu, saboda yawan Annabawan da suke cikinsu.**
**(33) Kuma muka basu hujjoji da dalilai, waxanda muka qarfafi Annabi Musa da su, wanda yin hakan ni'ima ce bayyananniya gare su, kamar ni'imar mannu (darva) da salwa, (Naman tsuntsun fakara) da wasun su.**
**(34) Haqiqa waxannan mushirikai, masu qaryatawa suna cewa, suna masu inkarin yiwuwar tashi bayan mutuwa:**
**(35) Babu komai face mutuwar mu ta farko, babu wata rayuwa a bayanta, kuma mu baza a tashe mu ba bayan wannan mutuwar.**
**(36) Ya kai Muhammad, kai da mabiyanka ku zo mana da iyayen mu a raye, waxanda suka mutu, idan har da gaske kuke yi cikin abin da kuke da'awa cewa: Allah zai tashi matattu da rai, don yi musu hisabi da bada sakamako.**
**(37) Ya kai wannan Manzo, shin waxannan mushirikai masu qaryataka, su ne mafi qarfi da kariya, ko kuwa mutanen Tubba, da waxanda suka gabace su, kamar Adawa, da Samudawa, dukkaninsu mun halakar da su, haqiqa sun kasance masu laifi.**
**(38) Ba mu halicci sammai da qassai da abin da yake tsakaninsu ba domin wasa da halittarsu.**
**(39) Ba mu halicci sammai da qassa ba sai don wata hikima babba, sai dai mafi yawan mushirikai basu san haka ba.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Wajabcin mumini ya koma ga Ubangijinsu domin ya tsare shi daga makircin maqiyinsa. 2 - Halaccin yin mummunan addu'a a kan kafirai, yayin da suka qi amsa kira, ko yayin da suke yaqar ma'abota gaskiya. 3 - Duniya bata yin baqin cikin mutuwar kafiri, saboda a wulaqance yake a wurin Allah. 4 - Halittar sammai da qassai don wata hikima babba, wadda karkatattun mutane suka jahilta.**

إِنَّ يَوْمَ ٱلْفَصْلِ مِيقَـٰتُهُمْ أَجْمَعِينَ ﴿٤٠﴾ يَوْمَ لَا يُغْنِى مَوْلًى
عَن مَّوْلًى شَيْـًٔا وَلَا هُمْ يُنصَرُونَ ﴿٤١﴾ إِلَّا مَن رَّحِمَ ٱللَّهُ ۚ
إِنَّهُۥ هُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلرَّحِيمُ ﴿٤٢﴾ إِنَّ شَجَرَتَ ٱلزَّقُّومِ ﴿٤٣﴾ طَعَامُ
ٱلْأَثِيمِ ﴿٤٤﴾ كَٱلْمُهْلِ يَغْلِى فِى ٱلْبُطُونِ ﴿٤٥﴾ كَغَلْىِ
ٱلْحَمِيمِ ﴿٤٦﴾ خُذُوهُ فَٱعْتِلُوهُ إِلَىٰ سَوَآءِ ٱلْجَحِيمِ ﴿٤٧﴾ ثُمَّ
صُبُّوا۟ فَوْقَ رَأْسِهِۦ مِنْ عَذَابِ ٱلْحَمِيمِ ﴿٤٨﴾ ذُقْ إِنَّكَ
أَنتَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْكَرِيمُ ﴿٤٩﴾ إِنَّ هَـٰذَا مَا كُنتُم بِهِۦ تَمْتَرُونَ
﴿٥٠﴾ إِنَّ ٱلْمُتَّقِينَ فِى مَقَامٍ أَمِينٍ ﴿٥١﴾ فِى جَنَّـٰتٍ وَعُيُونٍ
﴿٥٢﴾ يَلْبَسُونَ مِن سُندُسٍ وَإِسْتَبْرَقٍ مُّتَقَـٰبِلِينَ ﴿٥٣﴾
كَذَٰلِكَ وَزَوَّجْنَـٰهُم بِحُورٍ عِينٍ ﴿٥٤﴾ يَدْعُونَ فِيهَا بِكُلِّ
فَـٰكِهَةٍ ءَامِنِينَ ﴿٥٥﴾ لَا يَذُوقُونَ فِيهَا ٱلْمَوْتَ إِلَّا
ٱلْمَوْتَةَ ٱلْأُولَىٰ ۖ وَوَقَىٰهُمْ عَذَابَ ٱلْجَحِيمِ ﴿٥٦﴾ فَضْلًا مِّن
رَّبِّكَ ۚ ذَٰلِكَ هُوَ ٱلْفَوْزُ ٱلْعَظِيمُ ﴿٥٧﴾ فَإِنَّمَا يَسَّرْنَـٰهُ بِلِسَانِكَ
لَعَلَّهُمْ يَتَذَكَّرُونَ ﴿٥٨﴾ فَٱرْتَقِبْ إِنَّهُم مُّرْتَقِبُونَ ﴿٥٩﴾

آياتها ٣٧ — سُورَةُ الجَاثِيَةِ — ترتيبها ٤٥



**(40) Haqiqa ranar tashin alqiyama, ranar da Allah zai rarrabe a tsakanin bayi, wata rana ce da Allah ya yi alqawarinta ga halitta gaba xaya, zai tara su a cikinta.**

**(41) Ranar da makusanci baya amfanar makusancinsa, haka aboki da abokinsa, kuma ba za a kare su daga azabar Allah ba, saboda mulki a wannan rana na Allah ne, babu wanda ya isa ya yi da'awarsa.**

**(42) Sai dai wanda Allah ya jiqai daga cikin mutane, to shi zai amfana da abin da ya gabatar na aikin qwarai. Haqiqa Allah shi ne Mabuwayin da babu mai rinjayarsa, kuma mai hikima a cikin halittarsa, da gudanarwarsa, da kuma ikonsa.**

**(43) Haqiqa bishiyar zaqqum, wadda Allah ya fito da ita a tsakiyar wutar Jahimu.**

**(44) Abinci ne na mai babban laifi, shi ne kafiri, zai riqa ci daga 'ya'yan itatuwan ta munana.**

**(45) Waxanan 'ya'yan itatuwan kamar baqin mai suke, yana tafasa a cikin cikinsu saboda tsananin zafinsa.**

**(46) Kamar yadda tafasashen ruwa, da ya kusa qonewa don zafi yake tafasa.**

**(47) Kuma za a cewa Zabaniyawa: "Ku kama shi, ku ja shi da qarfi da tsanantawa, zuwa tsakiyar wutar Jahimu".**

**(48) "Sannan ku kwarara tafasashen ruwa a kwanyar wannan abin azabtarwar, kada ya rabu da azaba".**

**(49) Kuma za ce masa cikin qasqanci: "Ka xanxani wannan azaba mai raxaxi, haqiqa kai mai qasaita ne, wanda ba a isa a ravi wajenka a cikin mutanenka ba".**

**(50) Haqiqa wannan azabar, ita ce wadda kuka kasance kuna shakkun afkuwarta a ranar alqiyama, amma yanzu shakka ta gushe muku da ganin wannan azaba.**

**(51) Haqiqa masu jin tsoron Ubangijinsu, ta hanyar kamanta abubuwan da ya umarta, da nisantar abubuwan da ya hana, suna wani wuri, suna cikin aminci daga dukkan abin qi, ba zai same su ba.**

**(52) A cikin lambuna da qoramu masu gudana.**

**(53) A cikin Aljannah za su riqa sa alhariri maras kauri da mai kauri, sashensu yana fuskantar sashe, ba wanda zai kalli qeyar wani.**

**(54) Kamar yadda muka girmama su da abin da aka ambata, zamu aura musu kyawawan mata, masu yalwar idanun da kwayar idon take fara fat, gefenta kuma baqi wuluk.**

**(55) Suna kiran masu yi musu hidima, domin su kawo musu kowanne irin kayan marmari da suke so, ba tare da tsoron yankewarta ba, ko kuma ta cutarwa.**

**(56) Zasu dauwama a cikinta, ba zasu xanxani mutuwa a cikinta ba, sai dai mutuwar su ta farko da suka yi a duniya, kuma Ubangijinsu ya kare su daga azabar wuta.**

**(57) Duk wannan karamci ne da kyautatawa daga Ubangijinka a gare su, kuma wannan abin da aka ambata na shigar da su cikin Aljannah, da basu kariya daga wuta, shine babban rabo, wanda babu rabon da ya kai shi.**

**(58) Haqiqa mun sauwaqe wannan Alqur'ani, ta hanyar saukar da shi da harshenka na larabci – Ya kai wannan Manzo - ko sa wa'azantu.**

**(59) Ka saurari nasarar ka, da kuma halakarsu, domin su ma masu sauraron halakarka ne.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Za a haxawa kafiri azabar jiki da ta rai.**

**2 - Babban rabo shi ne tsira daga shiga wuta, da samun shiga Aljannah.**

**3 - Sauwaqewar da Allah ya yi wa lafuzan alqur'ani, da ma'anoninsa ga bayinsa.**

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

حمٓ ﴿١﴾ تَنزِيلُ ٱلْكِتَٰبِ مِنَ ٱللَّهِ ٱلْعَزِيزِ ٱلْحَكِيمِ ﴿٢﴾ إِنَّ فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلْأَرْضِ لَءَايَٰتٍ لِّلْمُؤْمِنِينَ ﴿٣﴾ وَفِي خَلْقِكُمْ وَمَا يَبُثُّ مِن دَآبَّةٍ ءَايَٰتٌ
لِّقَوْمٍ يُوقِنُونَ ﴿٤﴾ وَٱخْتِلَٰفِ ٱلَّيْلِ وَٱلنَّهَارِ وَمَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ مِنَ ٱلسَّمَآءِ
مِن رِّزْقٍ فَأَحْيَا بِهِ ٱلْأَرْضَ بَعْدَ مَوْتِهَا وَتَصْرِيفِ ٱلرِّيَٰحِ ءَايَٰتٌ لِّقَوْمٍ
يَعْقِلُونَ ﴿٥﴾ تِلْكَ ءَايَٰتُ ٱللَّهِ نَتْلُوهَا عَلَيْكَ بِٱلْحَقِّ فَبِأَيِّ حَدِيثٍ بَعْدَ
ٱللَّهِ وَءَايَٰتِهِۦ يُؤْمِنُونَ ﴿٦﴾ وَيْلٌ لِّكُلِّ أَفَّاكٍ أَثِيمٍ ﴿٧﴾ يَسْمَعُ ءَايَٰتِ
ٱللَّهِ تُتْلَىٰ عَلَيْهِ ثُمَّ يُصِرُّ مُسْتَكْبِرًا كَأَن لَّمْ يَسْمَعْهَا فَبَشِّرْهُ بِعَذَابٍ أَلِيمٍ
﴿٨﴾ وَإِذَا عَلِمَ مِنْ ءَايَٰتِنَا شَيْـًٔا ٱتَّخَذَهَا هُزُوًا أُو۟لَٰٓئِكَ لَهُمْ عَذَابٌ
مُّهِينٌ ﴿٩﴾ مِّن وَرَآئِهِمْ جَهَنَّمُ وَلَا يُغْنِي عَنْهُم مَّا كَسَبُوا۟ شَيْـًٔا
وَلَا مَا ٱتَّخَذُوا۟ مِن دُونِ ٱللَّهِ أَوْلِيَآءَ وَلَهُمْ عَذَابٌ عَظِيمٌ ﴿١٠﴾ هَٰذَا
هُدًى وَٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ بِـَٔايَٰتِ رَبِّهِمْ لَهُمْ عَذَابٌ مِّن رِّجْزٍ أَلِيمٌ ﴿١١﴾
ثلاثة أرباع الحزب ٥٠ ۞ ٱللَّهُ ٱلَّذِي سَخَّرَ لَكُمُ ٱلْبَحْرَ لِتَجْرِيَ ٱلْفُلْكُ فِيهِ بِأَمْرِهِۦ وَلِتَبْتَغُوا۟
مِن فَضْلِهِۦ وَلَعَلَّكُمْ تَشْكُرُونَ ﴿١٢﴾ وَسَخَّرَ لَكُم مَّا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي
ٱلْأَرْضِ جَمِيعًا مِّنْهُ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَءَايَٰتٍ لِّقَوْمٍ يَتَفَكَّرُونَ ﴿١٣﴾



# Suratul Jathiyah

An Saukar Da Ita A Makkah

## Daga Manufofin Surar:

**Magance matsalar masu son zuciya, masu yin girman kai ga gaskiya, ta hanyar bijiro da ayoyi da tunatarwa game da lahira.**

## Tafsir:

**(1) (Haa Mim) Bayani a kan ire-iren waxannan haruffa ya gabata a farkon suratul Baqara.**
**(2) Saukar da Alqur'ani daga Allah, Mabuwayi, wanda babu mai rinjayarsa, kuma mai hikima cikin halittarsa, da ikonsa, da gudanarwarsa.**
**(3) Haqiqa a cikin sammai da qassai akwai dalilai akan ikon Allah da kaxaitakarsa ga Muminai, domin su ne suke xaukan izina da ayoyi.**
**(4) Kuma a cikin halittarku – Ya ku mutane - daga xigon maniyyi, sannan daga gudan tsoka, sannan daga gudan jini, kuma a cikin halittar abin da Allah ya watsa shi na daga dabbobin da suke tafiya a bayan qasa, akwai dalilai a kan kaxaitakar Allah ga mutanen da suke sakankancewa da Allah ne mahalicci. (5) Kuma a cikin maye bayan juna tsakanin dare da rana, da abin da Allah ya saukar na ruwan sama, ya raya qasa da shi, ta hanyar fito da tsiro a bayanta, bayan ta kasance matacciya, babu tsirrai a kanta, da kuma sarrafa iska, ta hanyar zuwa da ita wani lokaci ta wani vangare, wani lokacin kuma ta wani vangaren daban, domin amfanin ku, akwai dalilai ne ga mutane masu hankalta, sai su kafa hujja da su a kan kaxaitakar Allah, da ikonsa a kan tashi bayan mutuwa, da ikonsa a kan komai.**
**(6) Waxannan ayoyi da hujjoji, muna karanta maka su - Ya kai wannan Manzo - da gaskiya, to idan basu yi imani da zancen Allah wanda ya saukar ga bawansa, da hujjojinsa, to da wane zance kuma bayan shi zasu yi imani, kuma waxanne hujjoji zasu gasgata?!. (7) Azaba daga Allah ta tabbata da halaka ga duk mai yawan qarya mai yawan laifuka. (8) Wannan kafiri yana jin ayoyin Allah a Alqur'ani ana karanta masa, amma sai ya ci gaba da abin da yake kai na kafirci da savon Allah, yana mai yin girman kai ga barin gaskiya, kai ka ce bai tava jin waxannan ayoyin da aka karanta masa ba, to - Ya kai wannan Manzo - ka ba shi labari abin da zai munana masa a lahirarsa, shi ne azaba mai ciwo da take jiransa. (9) Kuma idan wani abu daga cikin Alqur'ani ya isar masa, sai ya riqe shi abin yin izgili, yana izgili da shi, waxannan masu irin wannan siffa ta izgili da Alqur'ani, suna da azaba ta qasqanci ranar alqiyama. (10) A gabansu akwai wutar Jahannama, tana jiransu a lahira, kuma abin da suka tara na dukiya ba zai amfana musu da komai ba a wurin Allah, kuma ba zai kawar musu da komai ba, haka nan abin da suka riqa na gumakan da suke bautawa koma bayan Allah ba zasu amfana musu komai ba, kuma ranar alqiyama suna azaba mai girma. (11) Wannan littafin da muka saukar da shi ga Manzonmu Muhammad (S.A.W) mai shiryarwa ne zuwa ga tafarkin gaskiya. Waxanda suka kafircewa ayoyin Ubangijinsu, waxanda ya saukar wa Manzonsa suna da azaba mai tsananin ciwo. (12) Ya ku mutane, Allah kaxai ne ya hore muku teku don jiragen ruwa su yi tafiya a cikinsa, da umarninsa, kuma don ku nema daga falalarsa, ta hanyoyi neman halal daban daban, kuma ko kwa godewa ni'imar da Allah ya yi muku. (13) Ya kuma hore muku (S.W.T) abin da ke cikin sammai na daga rana, da wata, da taurari, da abin da yake cikin qassai, na daga qoramu, da bishiyoyi, da duwatsu, da wasun su. Haqiqa a cikin hore waxannan gare ku akwai dalilai a kan ikon Allah, da kaxaitakarsa, ga mutanen da suke tunani cikin ayoyin Allah, kuma suke yin izina da su.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Qarya da zarcewa a kan zunubi, da girman kai, da izgilanci da ayoyin Allah, siffofi ne na vatattu, kuma Allah ya yi alqawarin azaba ga wanda ya siffantu da su. 2 - Ni'imomin Allah ga bayinsa suna da yawa, daga ciki akwai hore musu abubuwan da ke cikin duniya, 3 - Ni'imomi suna lazimtawa bayi godiya ga abin bautawar da ya ba su waxannan ni'imomi.**

قُل لِّلَّذِينَ ءَامَنُواْ يَغۡفِرُواْ لِلَّذِينَ لَا يَرۡجُونَ أَيَّامَ ٱللَّهِ لِيَجۡزِيَ
قَوۡمَۢا بِمَا كَانُواْ يَكۡسِبُونَ ١٤ مَنۡ عَمِلَ صَٰلِحٗا فَلِنَفۡسِهِۦۖ
وَمَنۡ أَسَآءَ فَعَلَيۡهَاۖ ثُمَّ إِلَىٰ رَبِّكُمۡ تُرۡجَعُونَ ١٥ وَلَقَدۡ ءَاتَيۡنَا
بَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ ٱلۡكِتَٰبَ وَٱلۡحُكۡمَ وَٱلنُّبُوَّةَ وَرَزَقۡنَٰهُم مِّنَ ٱلطَّيِّبَٰتِ
وَفَضَّلۡنَٰهُمۡ عَلَى ٱلۡعَٰلَمِينَ ١٦ وَءَاتَيۡنَٰهُم بَيِّنَٰتٖ مِّنَ ٱلۡأَمۡرِۖ
فَمَا ٱخۡتَلَفُوٓاْ إِلَّا مِنۢ بَعۡدِ مَا جَآءَهُمُ ٱلۡعِلۡمُ بَغۡيَۢا بَيۡنَهُمۡۚ إِنَّ رَبَّكَ
يَقۡضِي بَيۡنَهُمۡ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ فِيمَا كَانُواْ فِيهِ يَخۡتَلِفُونَ
١٧ ثُمَّ جَعَلۡنَٰكَ عَلَىٰ شَرِيعَةٖ مِّنَ ٱلۡأَمۡرِ فَٱتَّبِعۡهَا وَلَا تَتَّبِعۡ
أَهۡوَآءَ ٱلَّذِينَ لَا يَعۡلَمُونَ ١٨ إِنَّهُمۡ لَن يُغۡنُواْ عَنكَ مِنَ ٱللَّهِ
شَيۡـٔٗاۚ وَإِنَّ ٱلظَّٰلِمِينَ بَعۡضُهُمۡ أَوۡلِيَآءُ بَعۡضٖۖ وَٱللَّهُ وَلِيُّ ٱلۡمُتَّقِينَ
١٩ هَٰذَا بَصَٰٓئِرُ لِلنَّاسِ وَهُدٗى وَرَحۡمَةٞ لِّقَوۡمٖ يُوقِنُونَ ٢٠
أَمۡ حَسِبَ ٱلَّذِينَ ٱجۡتَرَحُواْ ٱلسَّيِّـَٔاتِ أَن نَّجۡعَلَهُمۡ كَٱلَّذِينَ
ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ سَوَآءٗ مَّحۡيَاهُمۡ وَمَمَاتُهُمۡۚ سَآءَ
مَا يَحۡكُمُونَ ٢١ وَخَلَقَ ٱللَّهُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ بِٱلۡحَقِّ
وَلِتُجۡزَىٰ كُلُّ نَفۡسِۭ بِمَا كَسَبَتۡ وَهُمۡ لَا يُظۡلَمُونَ ٢٢



**(14) Ya kai wannan Manzo, ka faxawa waxanda suka yi imani da Allah, kuma suka gasgata Manzonsa: "Ku yafewa wanda ya sava muku daga cikin kafirai, waxanda basu damu da ni'imomin Allah ko azabar sa ba. Haqiqa Allah zai sakawa kowa daga cikin muminai masu haquri da kafirai masu qetare iyaka da abin da suka kasance suna aikatawa a duniya.**

**(15) Duk wanda ya yi aiki nagari, to sakamakon aikinsa nagari yana gare shi, Allah mawadaci ne ga barin aikinsa. Duk wanda ya munana aikinsa, to shi ma sakamakon mummunan aikinsa yana gare shi, munanawarsa bata cutar da Allah, sannan gare mu kaxai zaku koma a lahira, don mu sakawa kowa da abin da ya cancance shi.**

**(16) Haqiqa mun bawa bani-isra'ila Attaura, da yin hukunci a tsakanin mutane da ita, kuma muka sanya da yawa daga Annabawa daga cikinsu, daga zuriyar Annabi Ibrahim (A.S), kuma mun azurta su da daxaxan abubuwa na halal, kuma mun fifita su a kan mutanen zamaninsu.**

**(17) Kuma muka basu dalilai da suke fayyace gaskiya daga vata, ba su yi savani ba har sai bayan da hujja ta tsaya musu, da aiko Annabi Muhammad (S.A.W), babu abin da ya ja su zuwa ga wannan savani sai zaluncin sashinsu a kan sashi, don kwaxayin jagoranci da matsayi. Haqiqa Ubangijin ka – Ya kai wannan Manzo - zai yi hukunci a tsakaninsu ranar tashin alqiyama, game da abin da suka kasance suna yin savani a cikinsa a duniya, ya bayyana mai gaskiya da maras gaskiya.**

**(18) Sannan kuma muka sanya ka a kan wata hanya, da gwadabe, da tsari da umarnin da muka umarci waxanda suke gabaninka daga Manzannin mu, kana kira zuwa ga imani da aiki nagari, don haka ka bi wannan shari'ar, kada ka bi son zukatan waxanda basu san gaskiya ba, son zuciyarsu mai vatarwa ne daga gaskiya.**

**(19) Haqiqa waxanda basu san gaskiya ba, ba zasu kare ka daga azabar Allah ba da komai, matuqar ka bi son zuciyarsu. Haqiqa azzalumai daga kowane addinai da hanyoyi, sashensu masu taimakawa sashe ne, mai qarfafa shi ne a kan muminai. Allah mai taimakon masu jin tsoronsa ne, waxanda suke kamanta abubuwan da ya yi umarni, da nisantar abubuwan da ya hana.**

**(20) Wannan Alqur'anin da aka saukar ga Manzonmu haske ne, da mutane suke ganin gaskiya daga vata da shi, kuma shiriya ne zuwa ga gaskiya, kuma rahama ne ga mutanen da suke sakankancewa, domin su ne masu shiryuwa da shi zuwa ga tafarki madaidaici, don Ubangijinsu ya yarda da su, sai ya shigar da su Aljannah, ya nisantar da su daga wuta.**

**(21) Shin waxanda suka aikata kafirci da savon Allah da gavvansu suna tammanin mu sanya su daidai wajen sakamako da waxanda suka yi imani da Allah, kuma suka yi ayyuka nagartattu, ta yadda zasu yi daidai a duniya da lahira? Wannan hukunci na su ya yi muni.**

**(22) Allah ya halicci sammai da qassai don wata hikima babba, bai halicce su don wasa ba, kuma don a sakawa kowace rai da abin da ta aikata, na alheri ko sharri, Allah baya yin zalunci ta hanyar rage kyawawan ayyukansu ko qara munanan ayyukansu.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Yin rangwame da yafiya ga azzalumi idan bai bayyana varna a bayan qasa ba, kuma bai yi ta'addanci ga iyakokin Allah ba, yin hakan xabi'a ce mai kyau da Allah ya umarci muminai su aikata, in suna da kyakkyawan zaton hakan zai amfanar. 2 - Wajabcin bin shari'a da nisantar bin son zukatan mutane.**

**3 - Kamar yadda muminai da kafirai ba zasu daidaita ba a siffofi, haka ma baza su daidaita a wurin sakamako ba.**

**4 - Allah ya halicci sammai daidai da wata hikima babba, wadda karkatattu 'yan duniya suka jahilce ta.**

أَفَرَءَيْتَ مَنِ ٱتَّخَذَ إِلَٰهَهُۥ هَوَىٰهُ وَأَضَلَّهُ ٱللَّهُ عَلَىٰ عِلْمٍ وَخَتَمَ عَلَىٰ سَمْعِهِۦ
وَقَلْبِهِۦ وَجَعَلَ عَلَىٰ بَصَرِهِۦ غِشَٰوَةً فَمَن يَهْدِيهِ مِنۢ بَعْدِ ٱللَّهِ ۚ أَفَلَا
تَذَكَّرُونَ ﴿٢٣﴾ وَقَالُوا۟ مَا هِىَ إِلَّا حَيَاتُنَا ٱلدُّنْيَا نَمُوتُ وَنَحْيَا وَمَا يُهْلِكُنَآ
إِلَّا ٱلدَّهْرُ ۚ وَمَا لَهُم بِذَٰلِكَ مِنْ عِلْمٍ ۖ إِنْ هُمْ إِلَّا يَظُنُّونَ ﴿٢٤﴾ وَإِذَا تُتْلَىٰ
عَلَيْهِمْ ءَايَٰتُنَا بَيِّنَٰتٍ مَّا كَانَ حُجَّتَهُمْ إِلَّآ أَن قَالُوا۟ ٱئْتُوا۟ بِـَٔابَآئِنَآ إِن
كُنتُمْ صَٰدِقِينَ ﴿٢٥﴾ قُلِ ٱللَّهُ يُحْيِيكُمْ ثُمَّ يُمِيتُكُمْ ثُمَّ يَجْمَعُكُمْ إِلَىٰ
يَوْمِ ٱلْقِيَٰمَةِ لَا رَيْبَ فِيهِ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَعْلَمُونَ ﴿٢٦﴾ وَلِلَّهِ مُلْكُ
ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۚ وَيَوْمَ تَقُومُ ٱلسَّاعَةُ يَوْمَئِذٍ يَخْسَرُ ٱلْمُبْطِلُونَ ﴿٢٧﴾
وَتَرَىٰ كُلَّ أُمَّةٍ جَاثِيَةً ۚ كُلُّ أُمَّةٍ تُدْعَىٰٓ إِلَىٰ كِتَٰبِهَا ٱلْيَوْمَ تُجْزَوْنَ مَا كُنتُمْ
تَعْمَلُونَ ﴿٢٨﴾ هَٰذَا كِتَٰبُنَا يَنطِقُ عَلَيْكُم بِٱلْحَقِّ ۚ إِنَّا كُنَّا نَسْتَنسِخُ
مَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ﴿٢٩﴾ فَأَمَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ
فَيُدْخِلُهُمْ رَبُّهُمْ فِى رَحْمَتِهِۦ ۚ ذَٰلِكَ هُوَ ٱلْفَوْزُ ٱلْمُبِينُ ﴿٣٠﴾ وَأَمَّا
ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓا۟ أَفَلَمْ تَكُنْ ءَايَٰتِى تُتْلَىٰ عَلَيْكُمْ فَٱسْتَكْبَرْتُمْ وَكُنتُمْ قَوْمًا
مُّجْرِمِينَ ﴿٣١﴾ وَإِذَا قِيلَ إِنَّ وَعْدَ ٱللَّهِ حَقٌّ وَٱلسَّاعَةُ لَا رَيْبَ فِيهَا
قُلْتُم مَّا نَدْرِى مَا ٱلسَّاعَةُ إِن نَّظُنُّ إِلَّا ظَنًّا وَمَا نَحْنُ بِمُسْتَيْقِنِينَ ﴿٣٢﴾



**(23) Ya kai wanna Manzo, ka yi duba mana zuwa wanda yake biyewa son zuciyarsa, ya mayar da shi kamar abin bautawa, wanda baya sava masa, haqiqa Allah ya vatar da shi bisa ga ilimi, domin ya cancanci a vatar da shi. Kuma Allah ya rufe zuciyar sa, baya ji, jin da zai amfana da shi, kuma Allah ya sanya rufi a ganinsa, wanda yake hana shi ganin gaskiya, to wane ne ya isa ya datar da shi zuwa ga gaskiyar bayan Allah ya vatar da shi?!. Shin ba zaku tuna munin bin son zuciya ba ne, da alfanun aiki da shari'ar Allah?!.**

**(24) Kafirai masu inkarin tashi bayan mutuwa suka ce: "Babu wata rayuwar sai wannan rayuwar tamu ta duniya kawai, babu wata rayuwa bayanta, wasu jama'a suna mutuwa basa dawowa, wasu kuma jama'ar suna rayuwa, babu abin da yake kashe mu sai wucewar dare da rana. Basu da wani ilimi a kan musun tashi bayan mutuwa da suke yi, face dai kawai suna zato ne, zato kuma baya wadatar da komai a wajen gaskiya.**

**(25) Idan ana karantawa mushirikai masu qaryatawa da ranar alqiyama ayoyin mu bayyanannu, basu da wata hujja da suke kafa hujja da ita sai faxinsu ga Manzon Allah (S.A.W) da sahabbansa: "Ku raya mana iyayenmu waxanda suka mutu, idan har da gaske kuke cikin da'awarku ta cewa za a tashe mu bayan mutuwar mu". (26) Ya kai wannan Manzo, ka faxa musu cewa: "Allah ne yake raya ku da halittarku, sannan ya kashe ku, sannan ya tara ku bayan mutuwar ku a ranar alqiyama, don yin hisabi da bada sakamako, wannan ranar da babu wani kokwanto cewa zata zo, sai dai mafi yawan mutane basu san haka ba, don haka basa yi mata tanadi da ayyuka na qwarai". (27) Mulkin sammai da qassai duk na Allah ne shi kaxai, don haka ba a bautawa kowa a cikinsu da gaskiya sai shi. Ranar da alqiyama zata tsaya, wadda Allah zai raya matattu a cikinta, domin yin hisabi da bada sakamako a wannan rana masu vatanci waxanda suke bautawa wanin Allah za su yi asara, masu vata gaskiya, da tabbatar da varna. (28) Ya kai wannan Manzo, a wannan rana zaka ga kowace al'umma tana gurfane a kan gwiwarta, tana sauraron me za a yi mata. Kowace al'umma ana kiran ta zuwa ga littafin ayyukanta, wanda Mala'iku masu kiyayewa suka rubuta a kanta. A wannan ranar ne ake sakawa muku – Ya ku mutane - da abin da kuka kasance kuna aikatawa a duniya, na alheri da sharri.**

**(29) Wannan shi ne littafin mu, wanda Mala'ikunmu suka kasance suna rubuta ayyukanku a cikinsa, zai yi muku shaida da gaskiya, don haka ku karanta shi. Haqiqa mun kasance muna umartar Mala'iku masu kiyayewa suna rubuta abin da kuke aikatawa a duniya.**

**(30) Amma waxanda suka yi imani, kuma suka yi ayyuka nagari, sai Allah ya shigar da su cikin Aljannarsa da rahamarsa, wannan sakamakon da ya ba su, shi ne rabo bayyananne, wanda babu rabon da ya kai shi.**

**(31) Amma waxanda suka kafirce wa Allah sai a ce musu - don qara musu qunci -: "Shin ba a karanta muku ayoyina ba, amma sai kuka yi girman kai ga barin imani da su, kuma kuka kasance mutane masu laifi, kuna aikata kafirci da laifuka?". (32) Kuma idan a ka ce da ku: "Alqawarin Allah – wanda ya yi wa bayinsa na cewa zai tashe su, ya saka musu - gaskiya ne babu shakka a cikinsa, kuma alqiyama gaskiya ce, babu shakka a cikinta, ku yi aiki don haka" sai ku ce: "Mu ba mu san wannan lokacin ba, kawai zato muke, zato mai rauni cewa zata zo, amma mu ba mu da tabbacin cewa zata zo" .**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Bin son zuciya yana halakar da ma'abocinsa. 2 - Razanin ranar alqiyama.**
**3 - Zato baya wadatar da komai dangane da gaskiya, musamman a vangaren aqida.**